Duniya biyu mabanbanta[11/1, 11:41 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: _💫TWO DIFFERENT WORLD💫_

_*DUNIYA BIYU MABANBANTA*_

_BISMILLAHI RAHMANIR RAHEEM_

✍️ M SHAKUR

1️⃣

FREE PAGE
Ahankali yake saukowa daga stairs katafaren falon dako gidan shugaban kasa sai haka, yana sauka ahankali yana gyara zaman necktie din wuyanshi da hannu daya kasancewa dayan hannun na rikeda wata briefcase brown, daidai lokacin wata babban mace da a kalla zatai 57 tana sanye da shiga na alfarma tabude kofar wani daki wanda ga dukkan alamu kitchen ne sabida kamshin girke girke daya cika ko'ina tafito bayanta kuma wata maid ce dake sanye da uniform din masu aiki tana rike da babban warmer da alamu abinci ne aciki ta tsaya a bayan matan ganin uwar dakin nata ta tsaya itama, ganin matashin yasa batare data kalli maid dinba tace "kai kulan dining Shafa" sanan tacigaba da tafiya daidai matashin yakarasa saukowa daga stairs yakaraso gabanta, kafinma yay magana ta mika hannunta takai kan necktie din dayaketa fama dashi da hannu daya ta shiga gyaramai, dan murmushi yasaki cikin wata yar karaman natsassiyan murya yace "Barka da safiya Ammi" batare data amsashi ba ta sauke hannayenta kasa ganin tagama gyaramai ta kalli fuskarshi damuwa karara ya bayyana akan fuskarta amma saitai shiru batace mai komiba, kallon datake mai yasa adan shagwabe yace "Ammi, menen.....?" wuceshi tayi tai dinning taja kujera tazauna tadau mug tareda bude flask ta tsayaya ruwan zafi sanan ta waigo ganin har lokacin yana tsaye inda ta barshi yasa tace "anan zaka tsayane kana kallona ko ba break zakayi ba?"

Ayanda tamai maganan yasa yagane fushi take dashi kuma yasan dalilin fushin, karasowa yayi yaja kujeran gefen ta ahankali ya ijiye briefcase din hannunshi kan dayan chair dat is next to him sanan yazauna ahankali, mug din shayin dayasha kayan kamshi ta turomai gabanshi cikeda fushi tadau plate mai kyau fari kal kal ta debamai soyayyan Irish sanan ta kallai babu alamun wasa akan fuskarta tace "pepper soup ko ketchup? Wanne zan samaka?" murya chan kasa yace "ketchup" daukan bottle din ketchup tayi tabude tazubamai a gefen chips din dayawa dan tasan Allah yazubamai son ketchup sabida shi kadai agidan nan takesa ayo cefane harda na ketchup dan shi kadai kesha ita haryau abin baimata bane ko dandane batayi. Turamai plate din tayi gabanshi zata zare hannunta daga jikin plate din yakama hannunta yarike hakan yasa tadago idanunta ta kallai, dan shiru yayi yana kallonta sanan yadan sauke ajiyan zuciya asanyaye, murya chan kasa yace "I promise bazan dade ba kinji Ammi please" dan lumshe ido tayi cikeda takaicin shi sanan tabude su, batason tamai masifa hakan yasa ta sassauta murya tace "gobe fa bikinka haba Waleed bazaka iya daukan break kahakura da zuwa aikin nan ba, yakamata kaje kaga Ilham ko, you suppose kaje kaganta kaji medame dame take bukata, yaufa dinner ku mesa kake hakane? Kai baka gajiya da aiki, safe aiki, rana aiki dare aiki dukkai kadai bakagajiya?" tai maganan sounding a bit harsh sanan tai shiru tana kallonshi, ahankali ya saukar da kanshi kasa kaman bazaiyi magana ba saikuma yace "am doing all wat am doing for Dad Ammi, I'm doing it for him" yay maganan tareda dago kanshi ya kalli mahaifiyar tashi sosai yaga jikinta yay wani irin sanyi, hannunta takai ahankali ta shafa full sajenshi dakeda mugun laushi yana kyalli sosai tace "Waleed, Boy listen" tai maganan ahankali tace "I know u are doing all this for your father and trust me, I know duk inda mahaifinka yake he is proud of you cus he gave birth to such eloquent hard working youngman da burinshi shine yataimaki Al Umma, but in this Life Waleed you need to balance somethings, bazaiyu kullum aiki aiki aiki ba, u are needed awasu wajajen, za'ayi bikinka but bikin baya gabanka kwata kwata kabar su Khaleel da Hammad sumaka komi that isn't right kagane?" gyadamata kai yayi ahankali, sanan tace "abinda nakeso dakai yanzu, I know how much this work means to you dan haka bazan hanaka zuwaba, kaje but ana tasowa daga sallan juma'a kadawo kazo kafara shirye shirye, take a break of 2weeks aure zakayi kaji" gyadamata kai yayi amman harga Allah yasan yanada rai da lafiya bazai iya yaki zuwa wurin aiki harna tsawo kwana goma shahudu ba but bazai iya gardama da Ammi ba. "now eat karkai latti" maganan Ammi ya katse shi hakan yasa ya karbi fork din datake bashi ya shigacin Irish din yana dangwalawa a ketchup, yadanci badayawa ba yadau shayin ya shanye sanan ya goge bakinshi yatashi yana kokarin daukan briefcase din yace "ina Mum Ammi? Naje dakinta bata ciki" murmushi Ammi tayi tace "Mum dinka nachan ana harkan biki, ni banmasan ina tanayi ba, wuce katafi sabida kadawo dawuri" gyadamata kai yayi yadau briefcase din yafito waje, babban compound ne mai bala'in girma sai amsa gaisuwan masu aiki yake, gaban wata jeep yayi da wani mutumi katoto ke tsaye agabanta yana sanye da bakaken suit, yana ganinshi yabude mai baya hakan yasa ya shiga ya zauna, yamaida kofar ya rufe sanan yawuce ya shiga mazaunin direba ya kunna motar aka budemusu Gate suka fita.

Tafiyan wajen minti talatin sukayi kaman zasubar garin Abuja sanan direban yay horn agaban wani tangamemen Gate wanda sojoji guda hudu ke tsaye agaban wajen rike da bindigogin su da alamu gadi suke an rubuta WARBAI ORPHANAGE HOME AND HOME OF THE DISABLED (Gidan Marayu da Gidan Nakasassu) asaman tangamemen Gate din, sojoji na sarama motan alamun gaisuwa, aka bude gate din akayi daga ciki direba yaja motar suka shiga, titi ne har titi kaman sun shiga wani gari daban suka hau tafiya, manyan fulawowi sun ratsa dan dandamalin tsakiyan titin daya raba titin shiga da titin fita, babban wurine da girman shi zaiyi girman wani babban University, daga farko farkon babu wani gini ta wajejen sai sport yard, wajen kwallon, wajen buga long tennis, basket ball sune awajen, almost tafiyan 5 min sanan sukakai wajen wani tangamemen masallaci mai kyau gaske an rubuta WARBAI MASJID ajiki da larabci, sanan sai wani katon story building da aka rubuta Boys Section ajiki mai girman gaske, babu kowa agaban wajen sai wasu yan yara haka dake sanye da uniform na makaranta su kusan goma da wasu ma'aikata maza ke taredasu suna sanye da jeans saikuma riga dayakasance uniform ne dan yanada logo WARBAI ORPHANAGE HOME AND HOME OF THE DISABLED rubuce ajiki, yaran nakasassu ne dan wasu hannun guragu ne dasu, wasu idanunsu wani kala, wasu nada katon kai, wani kuma shanyayyen hannu saidai dukkansu atsaftace suke fes fes, kallo daya zaka musu kagane suna samun special kula, suna sanye da clean uniform da white sucks dinsu ga jakunkunan makarantan suke goyedashi da ko wanne akwai sunanshi ajiki sabida a dinga ganewa dan jakunkunan iri dayane sanan ajikin school bag din shima akwai logo orphanage home din akai, agogon hannunshi ya kalla ganin tara saura yasa anatse yace "stop the car" parking direban nashi yayi baijira yafito yabude mai ba yabude motan yafito cikin dan fushi dan yanayinshi ya nuna haka, yaran suna ganinshi sukahau ihu suna tsalle irin na yaran nan sukai wajenshi da gudunsu. "Teacher, Teacher, oyoyo" kowanen su burinshi yakamo hannunshi yarike kosu kamashi, murmushi yayi daya karama fuskarshi wani irin kyawu da cikan haiba, ahankali ya tsugunna dan tsayinsu yazo daidai cikin harshen turenci yace "Hello Children" suma cikin harshen turenci sukece "Hello Teacher" sosai yaran ke tsalle tsalle banda mutum daya cikinsu da yake kuka mara sauti sai hawaye yake sharewa da bayan hannu, maaikatan dake kallonsu cikeda girmamawa suka gaidashi. "Barka da shigowa Dr" bai tsaya amsa gaisuwan suba strictly yace "why are this children late? Maiya faru ba'a kaisu school dawuri ba?" daya daga cikin ma'aikatan ne yace "Dr gabaki dayansu basuyi homework bane antsaya amusu ne" "what happen da baku zauna dasu kun ko yamusu ba jiya? Kunzaci am paying you all ne dan kuyi yanda kukaga dama?" yay maganan babu wasa dan inhar kan yarane or duty nasu he can question, baya daukan raini, saisa suke mugun tsoronshi, cikeda girmamawa daya daga cikinsu yace "mun shafa'a ayakuri Dr, hakan bazai kara faruwa ba in sha Allah, dan Allah kayakuri" "sorry teacher" yaran suka fada ganin yanayin fuskarshi yanuna he's a bit angry, kasa magana yayi sabida sun bashi hakuri yadauke kanshi yamaida hankalin shi kan yaron dake kuka, tashi yayi ya daukeshi yace "why are you crying namiji?" murmushi yaron yayi yadaura hannunshi kan necktie dinshi yana kallo abin yama daukemai hankali, necktie din yakama yana kallon fuskar yaron yace "you like it?" gyadamai kai yaron yayi da sauri hakan yasa yay murmushi yace "okay zansa akawo muku naku anjima okay" washemai baki yayi yaron yayi cikeda jin dadi

hakan yasa ya saukar dashi kasa yace "a tafi school to, bye" "bye Teacher" suka fadi dukansu atare sanan suka wuce school ya tsaya yana binsu da kallo, babu abinda yake so kaman yaga he's the reason behind this innocent children smile, yakai kusan 5min yana kallon yanda suke tafiya suna wasa suna tsalle tsalle maaiktan na tattarosu sanan ya kada kai yawuce yashiga motar da direban yabude mai sanan yamaida yarufe yakoma gaba yaja motar sanan suka tafi.

Babbban gidan marayu ne da nakasassu, akwai wani dankareren building da aka rubuta kitchen and dinning ajiki, anan both ma'aikata da yaran gidan marayu ke zuwa suci abinci, wani babban story building ne dake kusada kitchen din shi kadai ne building din da aka katangeshi an rubuta girls section ajiki, sai ta dayan bangaren haggu wani babban school ne, akeai nursery har zuwa SS3 ga qualify teachers sanan akwai islamiyya inda kullum by 4 yara da manya zasu tafi islamiyya ai karatu 6 suke tashi kowa ya dawo gida dan lumshe ido yayi yana tunawa da mahaifin shi shi yasan he can never be like his father dan baitaba ganin the most generous person in this world like his father ba, baban shi nada taimako, ga son zumunci ga karfafama talakawa saisa bayan ya rasu he set up this orphanage home din in his memory dan lada yadinga kaiwa gareshi, setting it up wasn't easy within the first two yrs dayay establishing nashi government sukai approving sanan sukai licensing orphanage din dan a yanzu ko tsintar yara akayi saidai gwamnati subada izini akawo yaran gidan, sanan gwamnati nabada tallafi dudda baya bukatar tallafinsu he has morethan enough that can keep the orphanage running in the next hundred years.

Ahankali yabude idanunshi jin motar yay parking, budemai direban yayi hakan yasa yafito yana bin parking space din admin block din dayaji flowers da kallo komi looking neat a perfect kaman a dubai, wani guy ne fari dogo dudda baikai Waleed din tsayiba yafito daga wani office yana sanye da bakin suit da necktie awuyanshi, hannunshi rikeda wata pad ta apple yana saukowa daga dan stairs din da bazasu wuce guda 10 stair case ba dazasu sadashi da kasa yana tunkaran su, hannu ya mikamai yana murmushi irin ta tsokana dinan yace "Ango I didn't expect to see u here today na dauka sai anjima zamu hadu a dinner" dan hararan shi yayi yace "Mr P.A tell me wat we got today?" dan dariya guy din yayi yace "P.A badadi abakinka dan baka saba cewaba malam, better call me da sunan da babana ya yanka raguna biyu ya lakaba min ARHAM ABDULLAH" dan murmushi yayi daya mugun lobar da dimples dinshi yawuce shi yafara hawa staircase din batare daya juyoba yacigaba da tafiya a binshi, sanin bazai sake cemai komiba yasa yadan dan danna screen din ipad din dayake rikeda shi yana biyeda shi abaya yace "all right let's see wat we've got here" sanan yadan sauke ajiyan zuciya yace "okay Boss, you have five major abubuwa da zakayi yau, number 1 is zakai magana da company Tata marcopolo dakasa su aikomana da 5 marcopolo buses dazamuyi amfani dashi for excursion dazamuje yankari game resort next week, sai the second thing is zaka shiga theatre by 9 surgery yaron nan dakeda outgrowth awuyanshi, abu na uku is zamuje girls section we need to inspect bunk dinsu da Iyami tamana complain are due for changes, abu nahudu kanada meeting da all the employees bayan sallan juma'a by 2:30, sai last abunda zakayi shine letter

dakace zakama state government" gyadamai kai yayi daidai sun karaso gaban office dinshi, hannunshi yadaura ajikin wani glass haka dake manne agaban  kofar, wani blue wuta glass din yakawo sanan yay scanning hanunshi sanan kofar tabude ya shiga ciki Arham biyeda shi, babban office ne, hadadden gaske dan tsayawa bayanin shi is a waste of time, office ne dayasha office furnitures na zamani, suit dinshi yacire yay hanging akan wani designers hanger sanan yawuce yaja kujeran shi ya zauna, shikuma Arham ya zauna a kujeran baki yana facing nashi yana jiranshi yay magana yaji amsan shi, agogon hannunshi Waleed ya kalla anatse sanan ya saukar da hannun yace "by nine zan shiga operation din, I think you will handle waya da company Tata marcopolo, and u will handle inspection of the girls section bunks, meeting with all the employees should be prospone cus banda time yau, you should tell secretary ya tura musu message kan na daga meeting din till further notice, tura letter ma to state government I don't think bazai yuwu yau ba maybe jibi nasami time zanyi, zaka iya tafiya kaje kai aikinka" kallonshi Arham yayi hakan yasa yace "wat?" ahankali Arham yace "talk to me X-Man, I know something is wrong with you, talk to me yaushe muka fara boyema juna issues?" dan hararan shi yayi yadauke kai batare dayace komiba, "X-Man" Arham yakirashi ahankali, cikin dan fushi Waleed yace "how many times do I need to explain this to you P.A time for work should always be time for work, ba'a hada aiki da friendship, please go and do your job I pay you for it, we will talk anjima" cikin fushi Arham ya tashi daga kan kujeran dayake  kai yace "kasan problem dina dakai?" dago idanunshi dasuka dan chanza launi Waleed yayi ya  tsareshi dasu, cikeda jin haushin shi sosai yace "you are so weak but u hide under the face of rudeness, you know what? You sucks, kuma kar Allah yasa kafada lemme go and do job din da you pay me for it" yabugi table din da hannu yay kara sosai sanan yajuya zai fita, sosai yaji wani iri kiranshi yayi. "Arha......" bugomai kofan yayi hakan yasa ya lumshe ido tareda daura hannunshi kan saman goshinshi yana nishi ranshi duk abace saikuma yadaki table din yace "f**k!" dan gajeren tsaki yayi yatashi, wani kofa dake cikin office din yaje, hannunshi yasa kan kofar itama kaman wanchan kofar yay scanning hannunshi sanan yabude mai ya shiga ciki, hadadden dakine da babu abinda babu aciki, gaban wani fridge yaje yabude, kwalaban wine ne kala kala, dauko daya yayi yadau glass cup yakoma kan hadadden Italian bed din dakin yazauna, yabude wine din ya tsiyaya a cup ya ijiye kwalban akasa sanan yadau cup din yakafa abaki ya shanye, zare cup din yayi daga bakinshi yana yatsine fuska sabida daci sanan ya ijiye glass cup din ya kara kallon agogon hannunshi, ganin tara saura yasa yafito, fita daga office din yayi ko kadan ranshi ba dadi yay hanyar babban clinic din orphanage din sai gaidashi ake amma baiko iya amsawa. Direct office dinshi ya shiga ya chanza kayanshi zuwa kayan shiga theater sanan yafito ya shiga theater din.

[11/1, 11:41 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍️ M SHAKUR

2️⃣

FREE PAGE

Wajajen 12:45 yafito daga asibitin da akwai Dr and qualify nurses, yawanci in ya shiga ciki yaje ko operation zaiyi ko kuma wani critical issues ne da akai needing attention dinshi shine yake shiga ciki. Office dinshi yawuce yana shiga yaga wayanshi akan table inda yabarshi tana ringing, karasawa gaban table din yayi ya kalli screen din wayan Ilham yagani kan screen din hakan yasa yadauke kai yawuce ya shiga dakin dake cikin office dinshi, bathroom yashiga yawanko hannayenshi ya dauro alwala sanan yafito ya shirya cikin suit dinshi yabude kofa yafito daidai wayar tahau ruri karasawa gaban table din yayi yasa hannu yadauki wayan ya kalli screen din ganin Ammi ke kiranshi yasa ya danna yakai wayan kunnenshi. "yamukai dakai Son?" kasa magana ma yayi dan baisan me zaice mataba, kwafa Ammi tayi tace "anyway kanenka Abdul da Hasim sunzo although suntafi masallaci su dawo kaikuma sukazo nema sun gama komi na Hall din wai" ahankali yace "yanzu zan tafi masallaci daganan zan wuto gida" Ammi batace mai komiba ta katse wayan abinta, bude kofa yayi yafito yay wajen parking space direban shi dake hira dawasu ma'aikata awajen da sauri yataso yabudemai ya shiga cikin motar yarufo sanan suka wuce suka tafi, bai tsaya neman Arham ba dan yasan zasu hadu anjima kuma yanzu yasan aiki yake he's handling many things yau.

Wuraren 3 suka shigo anguwan su ganin yanda kofar gidansu ya cika da jama'a yasa yaja wata gajeruwan tsaki yadau wayanshi, number Ammi shi yay dailing ringing biyu ta daga zaiyi magana yaji muryan Mom tace "Dan Yaro kana ina?" dan shiru yayi kafin ashagwabe yace "Mom ina waje I can't come inside mutane sunyi yawa" dan dariya tayi tace "to miskili mai tsoron mutane tunda cinyeka zasuyi, sangamemen katon namiji dakai kana tsoron taron jama'a, sa direban ka yazagayo ta bayan layi zansa abudema Gate din wurin" "OK Mom" katse wayan yayi yacema direba "muje tabayan layi" jan motan direba yayi suka zagaya kafin ma su karasa sukaga har anbude Gate din Abdul da Hasim yagani suka bude suna ihu ango ango ango, samari ne dudda basukai shi girma ba amman suna yanayi dashi saidai yafisu kyau nesa ba kusaba, parking direba yayi sukuma suka shiga maida gate din suna rufewa, saukowa yayi daga motan ya ballamusu harara suka kwashe da dariya, Hasim yace "Ya Waleed muje ka chanza mun karbo maka kayanka kaci gayu wife dinka needs u" baice musu komiba yawuce ya shiga flat din wajen suna biyeda shi, anan falo ya barsu suna hayaniyan su baice musu kalaba yawuce bedroom, kayan jikinshi yacire ya shiga bathroom wanka yayi yafito daure da towel, ayanda yake tafiya zaka gane babu abinda kemai dadi, shafa mai yayi ya shirya cikin wata bugaggiyar shadda mai light ruwan toka ta mugun haska shi sanan yadau turare zai fesa yaji anyi knocking kofar saikuma aka bude aka shigo, wata mata ce fara babba sosai tai kama da matar dazu saidai bata kaita girma ba da manyanta ga dukkan alamu kanwarta ce, ahankali yace "Mom" murmushi tayi ta maida kofar dakin tarufe takaraso gabanshi tana murmushi sosai tana binshi da kallo tace "wow kaga yanda kai kyau kuwa Dan Yaro na, I wish mahaifin ka na

raye yaga wanan ranan da Walilin shi zaiyi aure, iyye kawo turaren kaga na fesamaka" karban turaren tayi daga hannunshi tashiga fesamai tana kallon fuskarshi ganin baya kodan murmushi, ajiye turaren tayi sanan takama kafadar shi ta zaunar dashi kan gado sanan tazauna gefenshi ahankali tareda saukar da ajiyan zuciya, hannunta tadaga tadaura ata bayanshi takamo kafadarshi hakan yasa ya kwanta da kanshi kan kafadarta ahankali sukai shiru tanajin yanda yake saukar da ijiyan zuciya sanan tafara magana. "dagani sai Adda umman mu ta haifa, Umma nada cikina Abban mu yarasu, awahale Umma tahaifo ni inada shekara 7 aduniya itama tarasu, wani mutumin anguwan mu, attajiri dake shiri da Abban mu kafin yarasu inji Adda shiya karbemu yacigaba da kulada mu ahaka marigayi mahaifinka daya kasance abokin shi yaga Adda ya aura lokacin inada shekaru 15 ta tafi dani gidan mahaifin ka, da ita da shi suka cigaba da rainona suna tarbiyantar dani nakasance nine first child dinsu, ahannun Adda nataso nai girma, tadauki lokaci mai tsayi kafin ahaifoka, Waleed kakosan dani da mahaifinka ne muka samaka sunan nan, Waleed" tai murmushi sanan tacigaba tace "u are everthing to me Waleed with a plus, nina raineka ita kanta Adda har mamakin irin son danike maka takeyi, saisa zakaci har yau bata taba kirana da Maman Hasim saidai takirani da Maman Waleed, na raineka na kula dakai to the extend ko numfashi ka fitar ina gane ta rashin lafiya ce kota farin ciki, Waleed I know Adda na sama dakowa, and nasan kowace irin hukunci tadauka a rayuwanka is for the best badan ta cutar dakai ba dan zan iya rantse maka kaine farin cikin mahaifiyar ka, kai kadai takesawa a ido taji dadi, u are her entire world, batada miji kaine komi nata, kasaki ranka, today is your day, auren ka akeyi, be happy, for once ka manta da wanan aikin Arham na nan I know yaron kirkin nan will handle everything, ka shirya kaje wajen Ilham kaji medame take bukata kabata bikinku ake, rabon dakeje wajen yarinyar nan zance anfi wata, haba Waleed so kake Adda tai fushi, kasaki ranka, and enjoy yarinyar nada hankali ga kyau, gata graduate, lawyer fa eh, kodan yanda Adda keson auren kaima saikaso, bakasan Adda nason tasami jika kota iya maida sunan mahaifin kaba, kome zakayi kasama ranka u are doing it for your mother wlh Allah zai baka ladan hakan, u are doing it for your mum, repeat after me I am doing this for my mother" dan shiru yayi kafin ahankali yace "I am doing this for my mother" murmushi Mom tayi tace "yauwa Dan Yaro, tashi to" tai maganan tana dago kanshi daga kan kafadar ta sanan ta sumbaci goshin shi ahankali kafin tasake shi, hulan shi tadauka ta shiga karyamai tace "ka kwashi kudin dazaka basu?" da sauri yace "su wa?" dan baisan suwa zaibama kudi ba, dan dariya Mom tayi ta kafamai hulan aka tace "zaka bama kawayen Amarya kudi suyi duk wata hidiman daya rage kagane" gyadamata kai yayi yatashi tareda bude drawer gefen gadon yadau kudi yan 1k rapa guda biyar yasa a aljihu Mom sai binshi da kallo take dan tadade bataga yay kyau hakaba kodan yawanci suit yake sawa oho, sanan yajuyo ya kalleta, murmushi tamai tace "muje" fitowa sukayi atare su Hasim na ganinshi sukahau ihu Mom takama baki tana kallonsu sanan ta kalli Waleed tace "ahhhh lallai Waleed kwana biyu baka lallasa marasa kunyan nan ba" harara Waleed ya watsa musu sanan yajefama Hasim key yace "let's go, u drive" tashi sukayi, Abdul yace "bye Mom" bye tamusu suka wuce suka fita gwanin ban sha'awa, Waleed na dudduba wayanshi ganin har yanzu Arham bai kirashi ba wanda inda normal ne da yanzu sunyi waya sama dasau uku, ijiye wayan yayi gefenshi yana yan tunane tunane, Hasim da Abdul sai hiransu sukeyi dan sune gaban mota har sukakai Wuse, agaban wani tangamemen gida sukai parking, shima gidan cikeda jama'a gate abude event ma akeyi dan sai raye raye ake, kashe motan Hasim yayi yajuyo ya kalli Waleed yace "ya Waleed kirata" wayarshi yadauka yay dailing

number data kirashi dazu dayay saving da Ilham, ringing daya aka dauka kafin yamayi magana muryan wata mace ta ratsa kunnenshi. "Baby, Hello Baby, Dr" batare daya amsata ba yace "muna kofar gidanku" wani irin ajiyan zuciya ta sauke da saida yaji daga wayan tace "Omg, innalillahi, Baby na da gaske kana kofar gidan mu?" jin yay shiru bai bata amsaba takuma san bazai bata amsanba yasa tace "okay okay, bari naturo Salima ta shigo daku, ni bana gidanmu ina gidan Anty, amaryan Dady the next house na gaban gidanmu, uhmmnm bari, bari Salima tazo ta shigo daku" tafada sounding super excited tsabagen murna, kasan cewa yasan gidan amaryan baban nata yasa yacema Hasim ya gangara gidan gaban gidansu, hakan akayi Hasim yay parking gaban gidan, ko minti daya basuyi da parking ba wata budurwa doguwan tafito tana sanye da wata atampan biki taci makeup tazo gaban motan taredasa hannu tai knocking glass din motar dan bata iya ganin mutanen ciki, bude mota su Hasim dake gaba sukayi suka fito, cikeda fara'a tace "sannu ku da zuwa ina yininku" cikin fara'a Abdul yace "kawayen Amarya ansha kyau" dan dariya tayi tace "ina Dr? Amarya nachan takosa ta daura mijinta a ido" duk dariya sukayi Hasim yabude mai kofa, anatse yafito dan ko kadan baida garaje yana dan daddanna waya dan sako yake turama Arham, binshi Salima tayi da kallo dan all this while labarin shi takeji bata taba sa Dr a idoba, now she see abinda Ilham tagani ta mutum mai, guy din yahadu. "Hi Dr" tai maganan ayangance tareda mai waving hannu, dagokai Waleed yayi ya kalleta saikuma ya dauke kai yamaida hankalin shi kan abinda yake typing awaya yace "Hey" faduwa gabanta yayi ayanda yayi maganan cikin izza akuma kasalance sai taji ya mugun cikamata ido ga shakkan shi dataji all at a time, juyawa tayi ta kalli su Hasim tace "to bismillan ku, ku shigo" ta shiga gaba su Hasim biyeda ita, saida yatura sakon sanan yamaida wayan aljihu yabisu yana taku dai dai suka shiga gidan, yan mata ne dayawa a compound din ana yan abubuwa, wasu na pictures wasu na cin abinci sunci gayu sosai kowacce tasha makeup suna ganin su Hasim akadau guda ango ango, dariya Salima tayi tabude musu kofar falon da tuni kowacce mace tafice babu kowa ciki agyare tsaf suka shiga ta nuna musu kujure, sanan tawuce kitchen drinks takawo musu na alfarma tadan saci kallon Waleed dahar lokacin wayanshi yake daddannawa tace "ga drinks kusha bari nakawo amarya" sanan ta juya tai stairs, wani daki tabude ta shiga inda wata kyakkyawan yarinya ke zaune akan kujera da a kalla bazata wuce 25-26 years ba ana mata makeup, tana sanye da wata doguwan rigan ashobi white dayay mata shegen kyau mai makeup din na daura mata head da kyau, tana ganin Salima tace "kin shigo dasu Salima?" gyadamata kai Salima tayi tace "eh suna falo, ke Khadija dama haka Dr naki yake? My God he is damn cute but yanada wulakanci sosai wlh" murmushi amaryan tayi tareda juya idanu tace "don't tell me u expect handsome rich guy mai status nashi yazama kaman all this random guys you use to know on the street? Angaya miki irinsu Mubarak dinki ne? Cheap guys?" ta bushe da dariya mai makeup din itama tafashe da dariya, ganin mocking dinta Ilham keyi yasa Salima ta tashi ko kadan bataji dadin abinda Ilham tamata ba, tasaba da halinta dan sabawa amma ta tsani tacimata fuska agaban wasu, ganin ta tashi zata fita batare data cemusu komiba yasa da sauri Ilham tace "me haka kekuma daga wasa dadina dake saurin fushi Salima, yakuri to pls dawo kinga fa ke zaki kaini kasa bai kamata na sauka kasa nikadai ba kekuma wai bazaki gama min daurin bane?" da sauri mai makeup din tadauki pin tana sosokewa a ashoken.

Dawowa Salima tayi ta tsaya akanta, karasa soke daurin tayi Ilham tamike ta kalli Salima ganin ta daddaure fuska yasa tawani fada jikinta tareda rungumota tace "dalla na face miki sorry please karki damu anjima zan baki labarin Dr kinji ni yanzu kiyakuri dan Allah" yanda duk takaiga fushi saida tai murmushi tace "shikenan" tace "kinga yanda kikai kyau kuwa kaman bakeba Ilham" murmushi tayi tace "yi sauri muje naga Dr dina" hannunta Salima takama sanan tabude kofan suka fita sau daya tasaci kallonshi ta sunnar da kanta kasa ganin bashi kadai bane, shi hankalinshi ma nakan wayan hannunshi yana danne danne yay wani irin kyau da saida taji gabanta yafadi hakanan taji wani kishi yataso mata yanzu duka matan dasuka cika gidan nan su ganshi ahaka, da kyar ta iya ta danne kishin suka cigaba da sauka daga stairs ahankali, Hasim ne da Abdul suka tashi suna murmushi "wow, Amaryan Ya Waleed" karasa sauko da ita Salima tayi tana musu murmushi sanan takaita harkan kujeran da Waleed ke zaune two sitter ta xaunar da ita a gefenshi tace "Dr ga amaryan ka nan nakawo maka yanzu kwa barni nahuta" maganan dayaji yasa yadan dagokai ya kallesu sanan yadauke kai, juyawa Salima tayi tai waving su Hasim tace "bari naje waje" da sauri Abdul yace "bari muma mubiyoki mubama love birds some  space" dan dagokai Waleed yayi ya watsa musu harara suka kyalkyace da dariya suka fice abinsu falon yarage dagashi sai Ilham dake zaune kusada shi dukansu sunyi shiru.

Almost 5min suna zaune basucema junansu komiba sanin zasu iya kwana ahaka bai cemata kalaba dan tasan magana wuya takemai yasa ahankali tamika hannunta dayasha lalle ta daura kan hannunshi daya ijiye kan laps dinshi ta kama hannun gam, atare suka dagokai suka kalli juna, tasake matse hannunshi dat feels so soft kaman hannun mace smiling, ahankali tace "Dr is our wedding are u not excited? I feel so happy because am getting married to love of my life, I love you so much Dr Waleed Warbai" tai maganan hawaye na gangarowa daga cikin idanunta, dauke kai yayi da sauri he don't really know abinda ma zai cemata, ko 1 single feeling baidashi akanta, ganin baice mata komi ba yasa cikeda son janshi zance tace "waye best friend din naka cikin wayan nan da kazo dasu?" ahankali yace "bayanan, this are my siblings" murmushi tayi tareda lumshe ido tana bala'in son jin yana magana, maganan shi dadi sosai wlh, voice dinshi bala'in dadi, murmushi tayi tace "yana ina shi? Maisa baizo tareda kaiba?" dan dagokai yayi ya kalleta suka hada ido sanan yace "I left him in the office you will see him later" gyadamai kai tayi cikeda sonshi tace "kayi kyau sosai" dauke kai yayi yace "thanks" yadanyi shiru saikuma yace "you look beautiful as well" wani irin cikakken murmushi tasaki cikeda jin dadi sosai tace "nagode Dr" sukai shiru, agogon hannunshi ya kalla sanan yadago kai ya kalleta hada ido suka sakeyi dan idanunta na kanshi har lokacin, hannunshi yatura cikin aljihu yaciro duka rapan kudin daya taho dasu ya ijiye mata akan cinya yace "use it for anything you need, will see you later" gyadamai kai tayi ya mike tsaye tashi itama tsaye tayi itama batai wata wataba tafada jikinshi ta rungume shi tsam tsam  murya chan kasa tace "thank you Dr, sai anjiman kaji" sanan tasake shi da sauri yajuya yafita daga dakin batare daya kalleta ba yafita daga gidan.
[11/1, 11:42 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍️ M SHAKUR

3️⃣

FREE PAGE
Wuraren 4 yafito daga office dinshi ko kallon office din Waleed baiyiba yasauko yay wajen hadaddiyar motarshi ya shige yaja motar yadau hanyar barin gidan marayun, agaban wani gida dan madaidaici mai kyan gaske yay parking ya sauko, shiga gidan yayi yabude gate din sanan yakoma mota yaja motar zuwa cikin gida, parking yayi sanan yafito yaje yamaida gate din ya kulle yana bin tsakar gidan da kallo dayasha flowers ga interlock akasa dudda gidan baida wani girma sosai but yanada kyau, karasawa yayi ya shiga flat babba kwara daya da shi kadaine atsakar gidan, bude kofa yayi ya shiga falon da babu kowa ciki sai TV dake aiki gawasu hadaddun setin kujeru dasuka zagaye falon suka karama falon haske da kyawu, wucewa yayi ya shiga wata yar corridor da dakuna uku ke ciki, ahankali yake tafiya har yakai gaban dakin dashine last room din corridor yabude kofar dakin ya shiga, dakine mai kyau sai kamshi yake, ga Royal bed aciki sai kujera daya 3sitter komi na dakin fari harda curtains din dakin, wani babban frame na hotonshi ne ajikin bango, rage kayan jikinshi yayi yawuce yashiga bathroom din dake cikin dakin, wanka yayo yafito ya shirya cikin wata yar 3quater da farin singlet yazauna kan gado, wayarshi dayaga tana dan kawo wuta yasa yagane anyomai message, mika hannunshi yayi yadauki wayar ya danna, sako yagani daga Waleed.
"Where are you My P.A🤣?" yay emojin dariya agaba alamun tsokana yake, tsaki Arham yayi ya cillar da wayan yay kwanciyar shi akan gadon tareda lumshe idanu yana sauke ajiyan zuciya.

"Arham" muryan wata yar dattijuwa ta kwalamai kira, "Arham" aka sake kiran sunan nashi ana bude kofar dakin gabaki daya, bude idanunshi yayi dasuka dan chanza launi dan bacci yasomaji, wata mata ce da a kalla zatafi fifty ta shigo dakin tana sanye da doguwan rigan atampa dayasha stone work hannunta rike da charbi, tsayawa tayi chak ajikin kofa tana kallonshi cikeda mamaki ganinma bacci yasoma yi shida keda biki saikuma tace "ka shigo gidan kafi karfin ka shigo ka gaidani ko Arham" murmushi yayi na rashin gaskiya yana kokarin tashi ya

zauna yace "yakuri Umma, danaga baki falo nasan kina ciki kina salla saisa nayo dakin straight dannai wanka, inayin wankan kuma shine na kwanta" gyadamai kai tayi alamun ta gamsu da bayanin shi tace "yana ganka adaki kaida yakamata kana tareda Waleed yanzu, banma dade da dawowa daga gidan nasuba munata yan aikace akace achan" shiru yayi baice mata komiba, hakanan ranta yabata wani abu ganin yasauke kai yasa tace "kai ba magana nake maka ba" juyowa yayi ya kalleta cikeda takaici yace "bazani bikin ba yaje yay bikin shi shikadai su Abdul samai komi" yanda yay maganan yasa Umma ta shigo dakin da kyau tayo kanshi tace "me kake cewa ne haka? Wai Arham maisa kai gabaki dayanka bahaggon mutum ne eh? Kadaisan Waleed bazai taba iya komi batare dakaiba ko? Kakuma fi kowa sanin cewa duk duniyan nan Waleed baida aboki saikai ko? Kana cewa su Abdul, wani irin su Abdul abinda zai fadamaka comfortably bazai taba gayama su Abdul kannenku ba, Arham abokin ka kokuma ma nace dan uwanka dakuka taso tare yau bikinshi shine zaka juyamai baya eh?" daure fuska yayi tamau baice komiba, ganin da gaske fushi Arham yake yasa ta zauna ahankali gefenshi, hannunta tadaura akanshi ta shafa kan ahankali cikeda lallashi kafin ahankali tace "maiya hadaku Arham? Kuda komu iyayenku bamu isa muji tsakanin kuba shine yau kakeso ajiku, maiya hadaku tell me" shiru yayi kaman bazaiyi magana ba saikuma yace "Umma Waleed is rude, very rude, yana controlling dina anyhow, yau ya shigo office so moody shine....." harya gama bama Umma labarin kallonshi take saikuma tai murmushi tareda sauke ajiyan zuciya tace "Arham nasha gayama ka chanza halin nan nak......." cikin fushi yace "dama nasan side dinshi zaki dauka saisa banso na gayamiki bama, nasan u will always support Waleed sabida sunada kud....." wani mugun kallo da Umma tamai yasa yakasa karasa maganan yasaukar da kanshi kasa yana wasa da yatsu, ahankali tace "Arham harga Allah am not happy da wanan dabi'un naka, abu kadan kadauke shi da zafi, Arham do I need to explain yanda yaron nan yake sonka? Saina fadamaka? Kaida bakinka kasha fadan Umma Waleed nasona, Waleed na sona, Arham akwai abinda Waleed baima aduniyan nan ba? He saw u on the street kana 7yrs old kana tallan ayaba, yaron nan kullum saiya fito yabika kuje ku saida ayaban tare kudawo, tun iyaye basu saniba har suka sani, Arham yaron nan Allah ya jikan mahaifinshi, Allah yakai haske kabarinshi saida yasa mahaifinshi by fire by force yasaka a school din dayake the biggest school a Abuja then, Turkish, adaukeku a mota adawo daku a mota, Arham kadawo dan gayu, kuka gama yasa kuka tafi same University a kasan waje ka karanta business administration shikuma medicine, baitaba aboki ba cus yasha fadamin Umma Arham is my everything, Arham is my blood, Arham is my this and dat, yaron nan kome zai saya kome za'a sayamai agida in ba'a sayo nashi da nakaba bazai karbaba, yaron nan bought this house for me, yasaimin car, handling everything that has to do with me, every end of the month saiyayo min har gobe dudda na nunamai yanzu kana aiki kanada kudin yimin komi but yaron nan yaki, yabaka job a inda yake shima, he carry u along a komi, in yananan he want to see u awurin with him, he did everything for us and look I will forever be grateful to Waleed har karshen rayuwa ta, dabadan Waleed ba da Allah kadai yasan inda muke yanzu maybe muna kwana a kasan gada, ankoremu agidan haya" tai dan shiru tana sauke ajiyan zuciya sanan ta nisa tace "menene aibun fadimaka dayayi cewa lokacin office lokacin aiki ne bana firan abota ba eh? Kowa dake da any dangantaka da Waleed yasan the way his world revolve around gidan marayun nan, kafi kowa sanin irin soyayyan dake tsakanin shi da mahaifin shi, bayan rasuwan shi yabude gidan marayun da sunan mahaifin shi, gabaki daya soyayyan dayakema mahaifin shi yay transferring nashi to gidan marayun ne,

Arham idan Waleed wants to do good I think u should be the number person dazai bashi support, banda haka just take a look shima yadamu yana ganina agidan yazo wajena ya tambayan kadawo nace bansani ba, yamaka text kakimai reply, Arham karage zuciyan nan dan Allah karage, yanzu tashi kaje ka shirya katafi he needs u komi na hannunka kaji?" gyadamata kai yayi ahankali, dan murmushi tayi tace "right from day one Waleed has been a rude person but ahaka ai ka kawomin shi Umma ga abokina remember? Ka girmeshi yakamata ace kayi amfani da hankalinka and understand him better than anyone, babba babba ne yarona" dariya yadanyi hakan yasa tace "ko kaifa I sauri ina jiran ka a falo" gyadamata kai yayi tawuce tafita shikuma yatashi ahankali zaiyi wajen wardrobe dinshi wayarshi tadanyi kara juyowa yayi yadawo wajen  yadauki wayan yabude sakon da sauri ganin Waleed ne.

_"okay okay, I get it, you want me to say those words right? Sorry blood I know I was rude dazun nan but hey! Don't put too much pressure on me I might break, Ammi ne tamin fada dazu da safen nan but I am sorry for taking it out on you, please kazo su Hasim are driving me nut am about to loose it_

Dan murmushi yayi ya ijiye wayan batare dayamai reply ba yadauko wata bugaggiyar farar shadda ya saka dan akwai kayan dinner dazusu saka anjima da night ya feshe kanshi da turare, sanan yadau makullan motan shi yafito, tuk kafin ya iso Umma ta kafe kofar corridor da ido fitowa yayi hakan yasa ta murmusa tace "abokin ango da kanshi, agama nashi dakafana zanje wajen Ammin Waleed dama ita ke goyamaka baya wlh kokai aure kona bama wanan bazawaran datazo takanas tafadamin tana sonka dan kaji" dariya yayi yace "habadai Big boy irina zaki sadaka dashi Umma" dariya dukansu sukayi tace "dalla bacemin daga gani nisai kuma gobe in Allah yakaimu zan koma gidan" "alright bye Umma" "bye" tamai waving hand yana fita daga dakin, motan shi ya shige ya zauna ya kunna motar sanan yafito ya bude gate yana tunanin yakamata yadauko mai gadi fa fa fitar da motar yayi waje yadawo ya kulle Gate din sanan yadau hanyar gidansu, dayake Umma tariga tafadamai ta bayan layi shima ya zagaya yay parking akofar gidan sanan ya kashe motan yafito yana tafiya dai dai yabude Gate ya shiga gidan, tundaga tsakar gidan wajen yakejin hayaniyan su Hasim girgiza kai kawai yayi yabude kofan ya shiga falon duk waigowa sukayi suna kallonshi, harara ya watsa musu hakan yasa suka fashe da dariya Hasim yace "ga best man din ango nan ya shigo, iyye see the glow" da hannu ya nunamai kunnenshi hakan yasa da sauri Hasim yace "tuba nake Ya Arham" barin falon yayi yadauki hanyar bedroom dinshi ahankali yabude kofa dakin nashi daga Mom har Waleed din datakai spoon bakinshi danya karbi abinci juyowa sukayi suka kalli kofan, ganin Arham ne yasa Mom tasaki wani murmushi, dauke kai yayi daga kallon Waleed din dayadan murmusa kadan ganinshi sanan ya karasa gaban mom  yadan rage tsawo cikeda ladabi yace "ina yini Mom" cikin wani irin jin dadi Mom tace "lpy lau Son, barka da zuwa, Allah yamaka albarka kaji, ina yawan fadama abokin ka ai duk duniya bazai taba samun aboki mai amana irinka ba ga girmama nagaba dashi, uwa uba ga kunya, kai Allah dai yabarku tare, kadinga hakuri da halin Waleed, dabi'un Waleed sai du'a'i jinshi yake kaman dan shekara biyu kagafa yanzu abincin nan wlh inda ban bashiba da bayici, ai nagode ma Allah yanzu zaiyi aure nahuta daman Adda tace ninenan nabata shi" tai maganan tana tallo keyanshi, yi yayi kaman zaiyi kuka saikuma yatashi ashagwabe yayi hanyar kofa da sauri Mum tace "ina zaka?" ahankali cikin yanayin maganan shi kaman na wanda yagaji yace "ni ruwa zan dauko" yana fadin haka yawuce yafita, ajiyan zuciya Mom ta dauka sanan ta maida hankalinta kan Arham dahar lokacin

bai tashi daga gabanta ba tace "Arham nasanka yarone mai hankali da sanin yakamata ga abokin kanan kacigaba da sashi a hanyar kwarai, kacigaba da hakuri dashi, ka girmeshi, Waleed is still a child kawai girman jiki dayake da shine yasa a kemai kallo kaman wani babba but har yanzu baikai 30ba kaima kasani, Arham always watch his back kaji dan Allah, kafishi wayau always guide him for us kaga shi kadai garemu, Allah muku albarka dukanku, bari kaga nakoma cikin gida in yazo ga abincin shinan kasashi yaci kasan matsalan shi na Ulcer pls, Ulcer shi yatashi batamai da kyau" gyadama Mom kai yayi ta tashi tawuce tafita, tashi yayi ahankali yana kallon hadadden bowl din da pepper soup din fish keciki ga plate na white rice da spoon komi anjera kan tray, girgiza kai kawai yayi yanabin ko ina nadakin da kallo kafin ahankali yadaga kafarshi yay gaban mirror dakin yana tafiya ahankali, tsayawa yayi yana kallon turarukan wajen, hannunshi yamika ahankali yadauko wani da shi kadai ne baisaniba cikin turarukan wajen mai suna "Men of Chastity" ya shiga jujjuya turaren yana kallo kaman mai wani tunani, bude kan turaren yayi yafesa kadan ahannun subhanallah saida ya lumshe ido tsabagen dadin kamshin, bude kofa da akayi yasa yajuyo da sauri rikeda turaren a hannu, Waleed ne ya shigo rikeda bottle water a hannunshi maidan sanyi, binshi yayi da kallo kafin idanunshi su sauka kan turaren da Ammi tabashi jiya as gift, dan murmushi yayi ya shigo dakin yace "wanan turaren kake kallo, Ammi tabani shi jiya da daddare gift, gama kwalin shi nan kasa dazun nan nabude shi" yamai pointing wani hadadden kwali dakenan kusada kafarshi ja akasa a ijiye, tsugunnawa Arham yayi yadau kwalin yadaura kan mirror sanan yabude kwalin ahankali, kwalin kadai abin kallo ne, har zai rufe kwalin idanunshi suka sauka kan receipt din turaren dake cikin kwalin idanunshi suka sauka kan kudin turaren 2.8m, da sauri yace "wanan turaren ne 2.8 million X-man?" batare daya kalleshi ba Waleed ya sauke goran ruwan dake bakinshi yace "eh kaima kaga bai tsada bako?" yafada yana daukan plate din rice trying to see in zai iyaci da kanshi dan bai koshi ba, sosai Arham ke binshi da kallo yama kasa magana he just wish inama ace shine dandan Ammi shikuma Waleed dandan Umman shi, Waleed dan gatane da baitaba ganin irinshi ba tarairayan shi ake kaman egg, bai dauki kudi anything ba sabida yanada su in excess ma, kaman ance yajuyo yajuyo gani yayi har lokacin Arham kallon turaren yake yamayi nisa a tunani dan murmushi yayi yamaida kanshi kan abincin yace "take it blood" maganan shi yadawo da Arham daga duniyan tunani yace "take wat?" cikin halin ko in kula yace "the pef" da sauri Arham yace "are u crazy? Ammi tabaka gift ne zaka wani ce nadauka" murmushi yayi yana chakalan abincin yace "ai itama tasan everything two ake saimin me and u maybe ta manta ne tasayo just one this time around, anyway take it will order akawo min wani" wani irin murmushi Arham yayi yataho wajen da sauri yadan bugi kafadar shi yace "thank you ango, angon Ilham"

dagokai yayi ya kallai tareda ballamai harara hakan yasa Arham yace "to me dalla, common chill, dan gatan Ammi I know yanda Ammi ke sonka dinan will choose the best girl for u, a princess kaman yanda kake a Prince to this family yar gata irinka" tabe baki yayi yatashi yace "nidai mutafi mosque" tashi Arham din yayi suka wuce suka tafi masallaci sallan magrib.

[11/1, 11:44 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍️ M SHAKUR

4

FREE PAGE

Direban gidansu Arham yatura dazasuje su dauko Amarya da kawayen ta to the event centre cus 9 za'a fara dinner dasu Hasim da friends dinsu, saida ya tabbatar sun tafi sanan yakoma cikin gidan, Waleed yasamu azaune kan kujera yana aiki da laptop dinshi ko ajikinshi kaman ba shine angon bikin ba, maida kofan Arham yayi yarufe ya karaso cikin dakin tsayawa yayi chak akanshi yace "muje ka shirya mutafi ai ba'a office kakeba yanzu kana gida" dan dagokai yayi ya kalli Arham din wata yar gajeren tsaki yaja yace "Omg wai why did u initiate this dinner stuff at the first place ma eh? Goddd! Mutum cannot rest again yayi abinda yakamata, am so so sick of this wedding, gosh!" girgixa kai Arham yayi ganin yanda yake masifa bil hakki ya karbe laptop din tareda shutting nashi down yarufe yarike ahannu sanan ya mikamai hannu yace "muje mushirya" ahankali yatashi Arham yabishi da kallo yana sanye da faran t-shirt sai wani 3quater short daya tsayamai wajajen gwuiwa shima fari, kafafunshi sanye cikin farin bathroom slippers, gashin kafarnan kwance lub lub irin na mugun dan hutun nan. Ahankali kaman wanda kwai yafashe wa aciki yake tafiya Arham yabude kofar hadadden bedroom dinshi suka shiga ciki, wajen wardrobe dinshi yayi yafito dawasu kaya da bama abude ba yazube su kan gadon sanan yabude ya shiga shiryawa cikin wata white suit na ermenegildo zenga, suit din yamugun fitting nashi daga kasan waje akamai order suit din aka tahomai dashi, sanan yadauki cover shoe dinshi na dinner sabo fil Black, designers shima na Testoni, tsayawa chak Arham yayi yana kallonshi yamugun yin kyau sai kallon kayan yake, juyowa Waleed yayi ya mikamai bow tie din dake hannunshi yace "tayani sawa blood" karban bowtie din Arham yayi yashiga samai kaman ba zaice komiba saikuma yace "amman wanan takalmin da suit din bashi mukaje muka sayo tareba a dunes ko?" girgiza mai kai yayi yace "Uncle yazomin dashi daga Ukraine jiya daya iso" gyadamai kai Arham yayi baisake cewa komiba yana gama samai yawuce yaje wardrobe yaciro wayanda suka sayo tare, yazaro tashi suit din black, dan abokan ango black suit zasu saka shikuma ango white, ya shirya tsaf sanan yataho key motar Waleed ya dauka yace "let's go" fitowa sukayi daga dakin, har zasu fita daga falon Ammi ta shigo dakin sun kusan cin karo, binsu tai da kallo yanda suka mata kyau sosai kafin ta sauke idanunta kan Waleed dayay mata wani irin kyau batasan lokacin data saki wani kayataccen murmushi ba, wucesu tayi tazauna kan sofa sanan takalli Waleed tace "zonan Son" tahowa yayi ahankali kaman wanda baison tafiya yazauna kusada ita inda take nunamai, hannunta takai tai cupping face dinshi tana kallonshi kaman yau tafara ganinshi kafin ta shafa fuskar tace "you look so much like your father today, kayi kyau sosai, Allah ya maka albarka kaji" dan lusme ido yayi yana danne abinda yakeji a zuciyan shi yace "Ameen" purse din data shigo dakin dashi ta ijiye agefenta tadauka tabude taciro rapas nayan dollars guda biyu tamikamai tace "gashi kama y'ata manni dasu" karban

kudin yayi ahankali dan baiso yaki karba taji haushi, rungume shi tayi ahankali taredamai kiss akumatu tace "stop being sad, I love you son, kaci abinci kuwa?" juyawa da sauri Arham yayi yafita daga dakin ya shiga mota Waleed din yay zamanshi a mazaunin direba, he just wish inama shine Waleed, kome zaiyi iyayen shi basa tabamai fada komin girman abun, unlike him da kullum abu kadan Umma fada takemai, abu dan kankani sai fada, Waleed ko abinci ma abaki ake bashi, bodyguard ma saida sukai fada da Ammi sosai dan anso kusan 10 sudinga binshi da kyar ya karbi daya wanda yadawo direban shi, bama abari yasha wahalan neman mataba aka samomai yar gidan masu kudi, graduate lawyer fa dudda dai bai taba ganinta ba aka bashi, just look at suit din da uncle dinshi ya kawo mai daga Ukraine, suit din ermenegildo yana costing about 22 to 28000 dollars, suit din jikinshi kadai worth a fortune dan yakai almost 8.8million naira a kudin Nigeria, takalmin kafanshi na Testoni kusan 3m ne shima, gata da dadi is beyond tunanin kowa ko shima inda bai gani da idanunshi ba dabazai taba yarda ana bama yaro gata irin gatan da ake bama Waleed ba, why was he born from the poor home? Maisa Umma ta auri Abban shi wani Malam Muhammad Bala, malamin islamiyya? Yataso ko gidan kansu basuda shi sai gidan haya, gidan dakuna ashirin da biyu da bayi guda biyu daya na kashi daya na fitsari, daga baya kuma yazo yarasu ya barsu cikin talauci, Waleed ne ya shigo rayuwan shi ya chanza mai komi..... Bude motan da akayi yadawo dashi daga daga dogon tunanin dayaje Ammi ne tabude ma Waleed din kofar motan tana kallon Arham tace "son ina gajiya" cikeda kunya dan yafi sakewa da Mom sabida ita tanada raha sosai while Ammi batada raha tanada fada, bata cika wasa da yaraba, aduniya in tana tareda Waleed ne kawai zaka dinga ganin dariyanta da murmushi ta abanza, da farkoma ya dauka bata sonshi ne sai daga baya ya lura haka Allah yayi ta ita kawai bamai yawan wasa da sakema yara fuska bane, cikeda girmamawa ya sauke fuskanshi yace "ina yini Ammi, ya taro" tana kokarin saka Waleed dake mata wani shegen shagwaba a mota tace "Alhamdulillah Arham, ai tuntuni muna tareda mahaifiyarka ma wlh, mamanka akwai kirki, kaga Arham gashinan drive him safe please, saikun dawo, bye Son, have fun okay, if u need anything ka kirani zan aikoma dashi" ta shafa kan Waleed din dake tura mata baki tana murmushi, kunna motar Arham yayi yaja Ammi na daga musu hannu tana murmushi, saida sukadan yi nisa ahanya sanan ya kalli Arham din dayaga yay shiru kuma ba halin shi bane yamika mai rapas din dollars din da Ammi tabashi duka biyun yace "use this" da sauri Arham ya kallai saikuma ya maida kanshi kan tukin yace "a'a, abinda Ammi tabaka zan karba" murmushi yayi kafin ahankali yace "take it inada wanda zanyi amfani dashi already" "shikenan" Arham yafadi ahankali kafin yace "thanks blood" murmushi Waleed yamai baice komiba, ahaka har suka karasa event centre babu wanda yakara magana cikinsu, daman yawanci in suna tare Arham ne mai kawo hira shi Waleed iya kanshi um a'a kokuma yan maganganu kadan, parking yayi yace "ka zauna aciki, I need to confirm in Amarya ta iso dan tare zaku shiga Hall din" bai jira amsanshi ba yamaida kofan yarufe yay wurin entrance din daidai zai shiga Abdul suna saukowa daga elevator tareda Salima suna hira shiru sukayi ganin Arham, Salima tace "you must be Arham ko? Best friend na ango" dan murmushi Arham yayi yana binta da kallo tana sanye cikin asshobi kawayen Amarya pitch yace "yeah nice to meet you Mss Salima" murmushi Salima tayi tana kallonshi ganinshi shima kyakkyawa sosai saidai dudda kyanshi baikai kyawun Dr ba, kuma Dr yafishi kaurin jiki da cikama mutum ido, ganin kallonshi take yasa ya katse shirun yace "ina Amarya? Cus they're going in together" "eh tana wani daki asama where is Dr?" juyawa yayi yace "lemme get him" har wajen motan yaje yabude

motan ya kalli Waleed dake dandanna waya yace "let's go ango" ballamai harara Waleed yasakeyi hakan yasa Arham yace "sorry mana ai kuma gaskiya nafadi kai angon ne"  ahankali Waleed yafito yana gyara suit din jikinshi su karan kansu su Abdul da Salima kallonshi suke yawani irin yin mugun kyau cikin white suit din dasukai mugun fitting dinshi maida kofar Arham yayi yana kallonshi yace "muje" ahankali suke tafiya har zuwa gaban entrance din Salima takasa daina kallonshi, dan kallonta yayi sanan ya kalli Abdul batare dayace musu komiba, anatse Abdul yace "sannu da zuwa Ya Waleed" bai kallesu ba yacema Arham dake kusadashi "let's go" wucewa sukayi dukansu suka shiga lift din yakaisu 4th floor, wani daki Salima tabude tana kallon Arham dan Waleed mugun cika mata ido yake tace "ku shigo tana nan" shiga ciki tayi suka hada ido da Ilham datasha uban gayu anmata makeup tasaka wani gown white daya mata fitinannen kyau ita kadai zaune kan wani Royal chair tai kyau sosai, cikin tafiyan nan nashi mai daukan ido daidai ya sawo kanshi cikin dakin Arham biyeda shi abaya, ahankali ta mike tsaye tana kallonshi hada ido sukayi hakan yasa ya tsaya chak shima, wani irin dadi ne ya lullubeta batasan lokacin data saki murmushi ba da sauri tazo wajenshi batai wata wataba tafada jikinshi ta rungume shi, ihu dakin ya dauka Arham ya shigo dakin da kyau yana kallonsu yana murmushi, da sauri Salima taciro wayarta tafara musu hotuna, ahankali yadaga hannayenshi ya rungume ta back, wani irin ajiyan zuciya ta sauke ta shige jikinshi sosai tana shakan kamshin dayakeyi, kaman ta jawo gobe takeji ayi a daura musu aure tayi ta dawo matar this ajebota handsome rich kid, "wai anan zamu kwana ne" Abdul yafada yana dariya, ahankali tasake shi cikeda jin kunya hakan yasa shima ya saketa, juyawa tayi suka hada ido da Arham da tundazu yake kallon bayanta Allah Allah yake yaga fuskarta, dan murmushi tayi sanan tajuya ta kalli Waleed din, dan lumshe ido yayi yabude kaman mai rada yace "my best friend, my brother, my blood, Arham" wani irin murmushi tayi ta juya ta kalli Arham tace "the great Arham nasha jin labarin ka tun abakin Ammi, my husband best friend childhood friend, so nice to meet you" dan murmushi Arham yayi yakasa daina kallonta yace "yes your husband is my blood we've been together since childhood, and he means the world to me, so ki kula min da abokina dakyau" dan dagakai tayi ta kalli Waleed kafin ahankali takama hannunshi tarike gam tana kallon face dinshi tace "I was born to do that, I love you so much Doctor na" ganin akwai mutane awajen yasa ahankali yace "thanks" wani iri Arham yaji he just feel inama shine yake da wanan soyayyan, Waleed is the definition of yaran da ake haifa da silver spoon abakin su, Waleed is just surrounded with love ne ta ko'ina, just look at yanda wanan hadaddiyar classic graduate lawyer yarinyar nan kesonshi tama mutu akanshi but yana yanga, infact baima sonta, baima son auren ko kadan, yarinya ga shegen kyau, itama yar masu kudi but yake yanga, he just wish zai sami yarinya haka dazata dinga mutunmai dinan, Salima ne ta katse silent din tace "I think we should go anfara event fa tundazu" fitowa sukayi duka atare, bayan an sanar da isowansu a hall aka kunna music suka shiga cikin kasa ita sai hotuna ake musu, sosai akai event kala kala duk in Ilham zata dagokai saita hada ido da Arham dake kallonta saidai ta sakanmai murmushi ta maida hankalinta kan Waleed, anso sai asuba za'a tashi 1 nayi Waleed kaman zaiyi kuka yakira Arham awaya bai dauka ba, ganin duk yay wani iri yasa Ilham tace "me kakeso baby?" batare daya kalleta ba murya chan kasa yace "nagaji i think atashi" ayanda yay maganan saida yasa har wani lumshe idanu tayi, Waleed is handsome gawasu mayun pink lips dayake dashi dake shinning kaman ka lashe, she can't wait to have a taste of them, kasa cemishi komi tayi sai binshi take da kallo, ganin kiss call dinshi yasa Arham yazo  gayamai yayi atashi yagaji

bacci yakeji, Arham baimai musu ba ya sanar da dj a kunne, yan abubuwa kadan akayi aka tashi, dudda yanda Waleed keso yaje gida Arham yace mai ba haka akeba shizai raka Amarya gida sanan saisu tafi, yanaji yana gani Arham yasa aka saka Amarya a bayan motansu yasa Waleed din kusada ita sanan yakoma gaba ya shiga ya tukasu, sun danyi nisa da tafiya Ilham ta matsa kusadashi ahankali tareda saka hannunta kan nashi ta kama gam, shiru yamata yana dan lumshe ido kafin daga baya bacci yay nasa ran kwasheshi ya daura kanshi kan kafadarta, wani irin dadine ya kasheta tai dan murmushi tace "haka abokinka keda saurin bacci?" ta glass din gaban motan ya kallesu yay dan murmushi yace "ai zakisha shagwaba, haka Allah ya yishi, mijinki shagwababbe ne" murmushi tayi ta shafa fuskarshi bata sake cewa komiba shima Arham haka har suka kai gaban gidansu, ahankali ta gyaramai kai tareda pecking nashi ta kalli Arham daya bude mata mota tace "good night our blood" murmushi yayi yace "good night our wife" gyadamai kai tayi tawuce yamaida kofan yarufe yana dan satan kallon bayanta, ta shiga gidan su, dakinta tawuce direct inda Salima da wata kawarta suke zaune harsun chanza kaya dansu tun dazu suka iso itakuma dayake ahankali Arham ke gudu saisa basu iso dawuri ba.
[11/1, 11:44 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍️ M SHAKUR

6️⃣

_*This novel is for free. Wanda mu Kungiyan FREE HAUSA NOVELS WATO BANZA *ASSOCIATIONS* muka dauki nauyin kawo maku.

Page 6

*_MOHAMMED V INTERNATIONAL AIRPORT, MORROCO._*

Karfe shida na safe daidai jirgin British Airways ya sauka a airport din Mohammed VI, sai kataniyar saukowa passinger suke daga cikin jirgin kana ganinsu kasan they're all stressed out sun gaji iya gajiya, saida kusan kowa yagama saukowa daga cikin jirgin sanan ahankali wata yar doguwan matashiya tasawo kanta tawajejen kofan zata fito tana goye da jakar makaranta abayanta tarike igiyoyin gefen jakan gam da hannunta, farace sol yarinyar tana sanye da wata

bakar doguwan riga mara kwalliya ko daya ajiki jallabiya, sai gyalen ta datai rolling aka sai abin yay kaman hijabi dudda hakan bai hana bakin suman gaban goshinta bayyana ba sun mugun kwanta sunyi lublub kaman na yar jaririyan da aka haifo yau, tanada manyan idanuwa fararen fat da brown kwaiduwan ido dan ko kadan nata ba bakake bane brown nesu light brown, giran ta full da gashi baki mai shining kaman ta sakamai relaxer, gawani siririn dogon hanci daya ratsa tsakiyan fuskanta ya bala'in karamata kyau, lips dinta pink yirr yan fele fele kananu kaman na yaron da aka haifa yanzu yanzun nan. Sake rike igiyan jakan datake goyedashi tayi gam, ahankali ta lumshe ido iskan garinsu yawani kada mata fuska tasaki murmushi daya lotsar da dimples dinta na both sides, dama da haggu sun lume chan ciki sosai kaman rijiya tai wani irin kyau da ba'a iya misaltawa sanan tabude idanun ahankali kafin tadaga yar kafarta tafara saukowa daga kan matattakalan jirgin tana kallon ko'ina ganin bataga yan gidansu ba daidai da mutum dayaba yasa taji wasu hawaye sun taho mata masu dumi, ahankali takai hannunta kan fuskarta zata share hawayen kaman daga sama taji an kwalamata kira. "Widad! Widad!" wani irin juyawa tayi da saurinta, wata mata tagani ita kadai tadan manyan ta sosai dan akalla zatafi 70 yar tsohuwa ce tana sanye da doguwan riga itama da hijabi  daya tsaya mata aciki tana tahowa da dan sandanta a hannu, wani irin tsalle yarinyan tayi hawayen suka karasa zubowa cikeda murna cikin harshen larabci tsohuwan tace "ahlan wa sahlan wa marhababik Widad" cikin wani irin muryan kuka yarinyar da tsohuwar takira da Widad tace "Assalamu Alaykum Amah" holding shoulders nata taohuwan tayi sanan tai kissing left cheek nata sanan tamata ana dama tana murmushi cikin tsantsan farin ciki da tsantsan so takara mata another peck a forehead tace "waallaykumus salam Widad, kaif? (how are you)" juyawa tayi tana kallon ko'ina na filin Airport din kaman mai neman wani abu tace "Alhamdulillah Amah" ganin yanda take kalle kalle yasa tsohuwar tai murmushi sosai batare datace mata komiba tabarta tacigaba da kalle kallenta, tana cikin kalle kallen kaman mai neman wani abu taji anrike mata hannu gam wani irin ajiyan zuciya ta sauke ta tsayar da kanta chak kafin ahankali lebbbenta suka furta "Ab.....Aby" dawani irin sauri ta juyo kaman amafarki, wani magidanci ne tsaye a bayanta yana rikeda hannunta yana sanye da jallabiya fari fat, kafanshi sanye da skos na maza, sai kanshi daure da rawanin larabawa sai farin gilas a idanunshi da daga gani kasan na kara karfin ganin idanune, kana ganinshi kaga tsantsan balaraben morroco kyakkyawa ajin farko, wani irin fashewa da kuka tayi haka Allah yayi ta tanada saurin kuka, very emotional mutum ce ita, sanan duk duniya batada wanda takeso  kaman babanta saisa kodaga nesa takanji a jikinta yana kusada ita, fashewa da kuka sosai tayi tace "Abyyyy"  anatse magidanci yasakin mata wani kyakkyawan murmushi yakai fararen hannunshi yadaura kan fuskarta ya share hawayen datake tass kafin yarungumeta ahankali yana bubbuga bayanta anatse irin na manya dinan cikin muryanshi na dattawa yace "marhababik, marhababik" sunkai kusan 5min tana jikinshi har lokacin tana sheshekan kuka sanan yadago ta, hannayenshi yasa akan fuskarshi yay cupping face dinta cikin tsantsan so yace "kidayra? (how are you)" ahankali tace "Alhamdulillah Aby" gyadamata kai yayi yace "masha Allah" yanuna mata mutanen dake tareda shi alamun ta gaidasu, ita sai a lokacin nema ta lurada su dazu mahaifinta kawai idanuwanta suka gane mata, yangidansu ne dan gidansu family house ne babban gaske, wata balarabiya dake kusada mahaifinta ta gaida ta hanyar cewa "Assalamu Alaykum Um" sanan ta kalli sauran tacemusu "Assalamu Alaykum" amsata sukayi ko wanne da murmushi kan fuskarshi banda matar dake kusada mahaifinta dako amsata batayiba, cikin harshen larabci mahaifin nata yace "mutafi gida"

kasancewan ansan koshi waye agarin saisama aka bari suka shigo har filin jirgin yasa suna zuwa akaimata clearing komi suka shiga wasu manya manyan jeep farare sukai gida, itadai tana cikin na mahaifinta kusada shi sai matar data kirada Amah gefen ta, mahaifinta kuma na gaba da direba, sukabar airport din.

Agaban wani babban tangamemen gida sukai parking, irin gidan nan da aka ginashi na usulin culture larabawa, an zagaye gaban gidan da flowers iri iri daban daban kalolinsu kaman kazo ka kwasa ka gudu, tun kafin tafito daga cikin mota takejin sautin ganga na mandiri ana bugawa ana wake, murmushi tayi ta kalli mahaifinta cikeda so duk lokacin dazata dawo daga school sai Aby yahada mata walima  na kayatarwa daban mamaki dan tarbanta kadai, bude kofa tayi tafito sanan tamikama kakanta hannu tafito daga motan Aby yafito yana kallonsu, kowa ya sassauko daga cikin motar akai cikin gidan, babban compound ne da girman tsakar gidan zaiyi girman primary school ana raye raye ana wake ana, ana rawa, ganin Widad din da iyayen ta sun shigo yasa mawakin yataho gabansu da yan amshin shi suna buga mandiri suna rera wake yace "kaifa Anti? Wa kaifa ji'iti? Marbabiki Ya Widad binti Othman Benjalloun" wani irin murmushi tayi ta washe fararen hakoranta tana kallonsu tana kara rike igiyan jakan makarantan ta abubuwa like this nabata peace sosai yanasa tana tunawa da mahaifiyar ta, ahankali mahaifinta ya kalli fuskarta murmushin dayagani kwance kan fuskar yasa yaji hankalin shi ya kwanta sosai, flowers ya karba a hannun daya daga cikin ma'aikatan gidan sanan yazo ta gabanta yabude flower ya sanya mata flower a wuyanta cikin harshen turenci dakeda Arabic intonation yace "wercome bark homer Widad" rungume mahaifinta tayi tana murmushi sosai tama kasa magana, ganin abun nasu bamai karewa bane yasa Amah cikin harshen larabci tace "to mayyar mahaifinta tadawo fa yanzu mun shigesu, saki ubanki muje daki kiyi wanka kizo ki chanza kayan nan kizo kici abinci ki kwanta kiyi bacci" Amah tai maganan tanajan hannunta, binta tayi tajuyo tama mahaifinta waving hannu sukai cikin gida, dan murmushi mahaifinta yayi yajuyo ya kalli matarshi datai kini kini darai cikin harshen larabci yace "kawomin shayi dakina" yay maganan tareda wucewa yashiga wani wakacecen falo irin traditional falon larabawan nan namasu kudin gaske, babu kujeru adakin sai wasu irin filulluka hadaddu set set da ake kishigada akansu gawani wargajejen hadadden carpet daya zagaye ko'ina a falon sai uban laushi kaman da fatar jirirai akayi sai shisha pot asalin pot din na larabawa, dan daidaikun asalin gidan rikakkun balarabe ne zakaje da bazaka ga shisha pot a dakunan su ba.

Othman Benjalloun dattijo ne dakeda shekaru 62 aduniya, bala'in mai kudine agarin morroco, agabaki dayan garin ance bayan Mohammed VI wanda yake number 1 mai kudin garin, Othman shine the second richest person in the whole morroco, yana harkan banking insurance, yanada bankuna yanada kasuwanci da dama, matayenshi uku aduniya, Mahaifiyar Widad itace ta farko wanda a yanzu ta rasu, sai matarshi da biyu wacce Widad takira da Umm, sai ta ukun wacce yasaka sabida cutar da Widad datasoyi Allah ya tona mata asiri, yarshi daya aduniyan nan tal

Widad, Allah baitaba bashi haihuwaba sai akanta, itama din harya cire rai dan yaga yay mata uku duk shiru yace halan daga shine sai kwatsam ga mahaifiyar Widad da ciki, yakusan karaman hausa a lokacin daya gane tanada ciki saisa da aka haifamai mace saiya radamata suna WIDAD ma'ana love, yana bala'in son yarinyar so mai zafi, gashi kana ganin yarinyar kaganshi kaman yay kaki, ko office zashi da yarshi da mahaifiyar ta yake zuwa sabida yadinga sata a ido kodayaushe, indan tafiyan fitanshi daga gari ce ta taso saidai yadauki mahaifiyar ta da ita dan bazai iya nisa da itaba saisa itama yarinyar ta taso tana bala'in son mahaifinta, tanada shekaru 18 mahaifiyar ta tarasu daga ciwon kwana daya tal, Widad takusan hauka take mahaifin nata yafita da ita da kyar aka samu taji sauki aka dawo da ita gida tadinga kuka daga karshe taroki mahaifinta tunda tagama sakandire yakaita wata kasar tai University intana gida tunawa da mahaifiyar ta take sosai, da kyar da kyar saima dayaga ta kwanta tana ciwo sanan ya yarda yakaita Egypt yamata komi yasaman mata admission in datake karanta mass communication.

Wani hadadden babban daki suka shiga itada Amah dake upstairs, dakin wakacece ne babba dayasha carpet tako ina mai bala'in kyau dan duk wanda yasan morroco yasansu da sana'ar kera carpet su sayar, gadaje biyune hadaddun gaske masu rumfa da aka zagaye da labulaye farare masu kyau acikin dakin babba da karamin gado, tun bayan mahaifiyarta ta rasu tadawo dakin kakanta da zama kakanta ne kadai takejin dadin zama da ita dan tana sonta kaman ne, jakanta tacire ta ijiye akasa sanan ta taka zuwa gaban wardrobe din dakin dan neman kayan dazata saka, Amah kuma ta ijiye sandarta agefe ta zauna ahankali kan gadonta tanabin bayan Widad din da kallo, shekara daya kacal dabata ganta ba amman saitaga ta chanza mata a ido sosai, dan murmushi tasaki tana tunanin Widad da aka haifa jiyane ta girma haka, batare da Widad tajuyo ta kalleta ba cikin harshen larabci tace "Amahh why are you smiling? Tunanin me kike?" tai maganan tareda juyowa hannunta rikeda wata jan kaftan dayasha ado kaman irin dogayen rigunan India, hararan ta Amah tayi tace "wuce kije kiyi wanka, favourite dinki nasa aka dafa tagine, rice da herbs saikuma flat bread" washe baki tayi ta yarda rigan hannunta kan gado da gudu tai bayi, kyalkyacewa da dariya Amah tayi tadauki sandarta tawuce tafita dan tabbatar da yan aikin sun jera komi a tsakiyan falon barinma wanda tasan yar jikallenta tafiso. Dan aikin datagani awurin yana ijiye plate dake dauke da dry fruits tacema "ina flat breads din danasa ku gasama Widad?" cikeda girmamawa yace "yanzun nan jibril zai karasa baking dinsu yafito dasu" zata sake magana taga Aby na saukowa daga sama shima da hannu tama dan aikin alamu daya wuce  yabata wuri, da sauri yawuce bayan ya gaida Aby, saukowa daga benen Aby yayi yazo gabanta mahaifiyar tashi yace "Assalamu Alaykum Amah" "waallaikumus salam" ta amsashi tana zama, ahankali shima ya zauna gefenta yadau inibi daya yajefa abaki yanadan bin wakan da akeyi awaje cikin kwanciyan hankali, ganin yanda yake farin ciki yasa

mahaifiyar shi takira sunan shi. "Othman" anatse yajuyo ya kalleta tareda ijiye inibin daya so jefawa cikin baki kan faranti, dan gyara zama Amah tayi da kyau kaman yanda shima ya natsu yana jiran yaji mezatace mai, cikin muryanta na tsofaffi tace "wace shawara ka yanke akan maganan damukai dakai jiya?" fuzar da iska yayi fuskarshi ya dan nuna damuwa yace "I don't know Amah, all I know for sure is bazata koma wanan makarantan babu aure akanta ba, ai nai mata kokari dana iya nabar y'ata wacce ita kadai ce Allah yabani aduniyan nan taje chan wani kasa tana karatu ba, banda hakama Amah bakiga yanda alamomin girma suka bayyana ajikinta sosai ba?" gyadamai kai Amah tayi cikeda gamsuwa da bayaninshi tace "nagani" yace "burin kowani mahaifin ya killace yarshi intana wanan matakin ya aurar da ita, na kashe all meetings danake dashi throughout this week, hutun sati biyu kacal gareta, nariga na sanar da iyayen Ahmad zasuzo anjima da daddare we are having engagement ceremony tonight, nikah zai biyo baya nanda sati in 7days time dudda a al'adance yakamata bayan engagement ceremony da shekara ne ake biki but I can't wait that long" ya karashe maganan ahankali saikuma yasaki dan murmushi mai kama data bakin ciki ya kalli Amah yace "Amah anya zan iya rayuwa kuwa in bana ganin y'ata?" yasakeyin murmushi hawaye na taruwaa idanunshi yace "Amah bantaba fadamiki wanan ba sabida nasan fada zakimin kice nabar yarinya tai concentrating a karatu kaza kaza kaza, kinkosan cewa ban taba kaiwa sati daya cur batare danaje Egypt ba dukko nisan shi?" ware ido Amah tayi cikeda mugun mamakin shi dan tasan dan danta business man ne yana yawan tafiye tafiye but bata taba sanin haka yake zuwa wajen Widad a makarantan ba frequently ba, one thing she knows for sure shine she always wondered ayanda Aby keson Widad kaman zaiyi hauka ya iya hakura hartai shekara a makaranta bai gantaba, maganan shi ne ya yanke mata dogon tunanin dataje yace "kinsan yanzu intai aure bazan iya dinga zuwa haka ina ganota bako" ya share hawayen dayadan zubomai da sauri yay murmushi yace "Amah banson ko kadan Widad ta wahala aduniyan nan, saisa nake aiki nake neman kudi sabida ita, dazaran na aurar da ita I believe lokacin tadawo cikakiyar mace, zanyi handing all over my properties, companies komi da komi nawa, all my assets to her ni zanyi retire na huta, shi will be managing everything, komi da komi dana mallaka nata ne Amah dan banda wani magaji aduniyan nan sai ita, I make sure nabata komi ranan da aka daura aurenta agaban mijinta da kowa, innai haka hankalina zai kwanta dan nasan tanada komi bazata taba wahala ba, yakika gani Amah?" kumatun shi Amah taja cikeda murmushi tace "brilliant thought, kasan I'm always proud of you Othman kai d'a ne nagari mai adalci, ina mai goyamaka baya dari bisa dari akan wanan hukuncin daka yanke, mu munriga munyi rayuwanmu aduniyan nan, munci duniyan mu da tsinke, mutuwa yauko gobe takan iya daukanmu, inhar bamu bama Widad da yanzu tafara girma komi damuka mallaka ba maimuka yi?" dan murmushi tayi tace "nima zinaruka na tunna lokacin aurena da mahaifinka, gabaki daya daman ita nakema ijiyansu ranan aurenta da izinin Allah zan bata, Allah yamaka albarka Othman Allah kuma yasanya ma auren albarka, na yarda da Ahmad sosai, nakuma san yanda yake sonta tun tana yar yarinya" dan dariya Aby yayi yace "kinsan mahaifinshi yacemin daya fadamai maganan engagement din danayi yakusan suma kinji fa yarinta" "ba yarinta bane tsabagen so ne da kauna ta gaskiya" suka kwashe da dariya irin ta manyan nan kafin tai hugging nashi su a dariya atare gwanin ban sha'awa.
[11/1, 11:44 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍️ M SHAKUR

5️⃣

_*This novel is For free. Wanda mu kungiyan *FREE HAUSA NOVELS WATO BANZA ASSOCIATIONS* MUKA DAUKI NAUYIN KAWO MAKU.

AYI KARATU LAFIYAAAAAAA

page 5

Bathroom tawuce dan shegen fitsari takeji, fitsari tayi sanan ta tube gown din jikinta tayo wanka gabaki daya tasaka bathrobe tafito tana kulle igiyan, zama kusada Salima tayi tana murmushi tace "I am so happy wlh, ina cikin tsananin farin ciki, am getting married to the man dat I love, wai kunga yanda Dr dina yay kyau kuwa" tai dan murmushi tana kallon lallen kafarta kaman mai tunanin wani abu tace "Dr na is so cute and duk mutanen dayake mu'amala dasu haka suke da kyau suma, just look at his best friend, shima yanada kyau wlh, so handsome saida baby na yafishi kyau nesa ba kusa ba" tai murmushi tareda danyin fari da idanu, dariya Salima da dayar kawarsu mai suna Nana sukayi dan is so obvious sonta yafi nashi yawa dat is inma yanason nata kenan, Nana tace "Ilham kinason Dr ki sosai wlh, har yanzu baki bamu labarin shi ba, waye shi a ina kuka hadu?" dagakai tayi tana kallon Pop dakin saikuma ahankali ta kwanta kan gado ta daura kanta ka hannayenta ta sauke ajiyan zuciya tace "Mummy na da Ammi (Maman) Waleed are gud friends very good friends, so su suka hadamu, parents dinmu suka hada auren maman shi na sona sosai, ita batason her only son ya auri any kind of girl saidai girl din da she trust sabida kar a cutar mata da yaro, tana sona sosai and taga nagama karatu na, inada good career ga kyau ga brains, gani yar aminiyarta saisa tace am the best choice for her son, that's that for that" tai dan murmushi taredayin tafi, Salima tace "to bamu labarin Dr" dan juya idanu Ilham tayi tareda gyara kwanciya tace "uhnnn Waleed baida wani much story to tell cus shiba loud person bane, baida hananiya, baida surutu sanan baya keeping friends, Arham shi kadaine abokin shi aduniyan nan" tasake yin shiru sanan tace "bayan su Mummy sun gama kulle kulle su kan zasu hadamu aure, sai wata rana Ammi ta aiko Waleed musamman danya kawo wasu

kaya wajen Mummy na, itama Mummy na cus komi plan ne nita tura waje bayan ya iso tace na shigo dashi falo na karbi sakon, ina fita waje, Oh Allah" tai dan shiru sanan tace "wlh I've seen many men, many guys, yara masu kudi nayan gayuma, yaran baze da nile tun ina University but bantaba ganin one like Waleed ba, I saw a very tall full guy fari in complexion, ko kadan baida rama jikinshi acike, yana sanye da cooperate dress da alamu office zashi a ranan, wani farin riga ne ajikinshi da bakin wando yasa wani blue and white necktie, yanada full saje da gemu baki sidik, gemunshi a mugun gyare baida yawa sosai yana kyalli tsabagen gyaran dayaji, lips dinshi pink yirrr kaman zaka taba jini yafito look perfect a face dinshi and moist kaman ya shafa lip balm, gashi da dogon hanci idanunshi manya sosai yanada perfect black eyeballs, giran shi acike bakin kirin, gashin kanshi nada dan yawa ba chan chan ba gashin kanshi na kyalli kaman irin na larabawan nan, he don't really look Nigerian, dana ganshi kasama motsi nayi sai shi daya luradani yacemin cikin sassanyar muryan nan nashi Mummy na nan, Ammi sent me, yanda yake magana ko dole yatafi da imanin kine, yanada broadfull chest, that is it fa, bayan na karbi sakon da sauri mai dakin Mummy na nace Mummy waye wanan yaron, tacemin his name is Dr Waleed Warbai 28yrs of age, only son din Mrs Warbai kawata, yamin ina sonshi cus mamanshi naso tahadani aure dashi ne, wlh ko I was just blushing, I couldn't believe abinda naji bansan lokacin dana fada jikin Mummy ba ina murna dudda tsakanina dashi is just 2yrs ne cus 26 nake shikuma 28 ban damuba dan he looks older dan his age irin yaran yan gayun nanne dasuka ci dadi suka fashe, a hakan ma dan yana gym ne saisa kibanshi baiyi yawaba it looks perfect on him, shikenan aka bani number shi sanan yakanzo once in a while, this boy is rich, his late dad is multi billionaire, babanshi nada companies, yanada company building boat na ruwa, and his father was the first person dayakawo electronic car a Nigeria, baban shi mahaifin shi, that is his grandfather balarabe ne matanshi yar Nigeria saisa Waleed inji Ammi da babanshi yake kama, kanin babanshi daya a duniya yana Ukraine shima kudine dashi sosai but baida yara shima saisa Waleed keda gatan duniya, his uncle nasonshi kaman me, all kudaden da mahaifinshi yabarmai he use them yabude gidan marayu, akwai hospital agidan marayin da nakasassun, akwai school tundaga nursery har secondary kuma duk wanda wish to further yana kaisu University, insuka gama yabasu aiki in sunason suyi aiki gidan marayun yayi in a outside nema yabasu sanan yamusu aure, matan inhar sunada tsayaye yana aurar dasu tun kafin ma su shiga University, as small as Waleed but taimakon dayake ko mahaifina baya irinshi, na auri someone like Waleed na haifama family su magaji nida talauci har lahira saisa dazaran na shiga gwaranni zan dingayi ko Mummy ma haka tafadamin haka zan dinga yi, to shikenan labarin and I can't wait for tommorow muyi aure, can't wait to make luv to my Waleed, shagwabben mijina" dariya duk sukayi haka suka dinga hira har bacci yay awon gaba dasu.

***

Ance rana bata karya saida uwar diya taji kunya, yau asabar dubbannin jama'a ciki harda gwamnoni da representative na shugaban kasa, dan ansan marigayi mahaifin Waleed, sanan har gobe suna business da companonin shi aka shaida daurin aure tsakanin Waleed Warbai da Khadija Ilham Maifanko akan sadaki 3million naira.

Sosai idanunshi sukai jaa sosai, kasa amsa gaisuwan yan uwa da abokan arziki yayi, ga employees dinshi sun cika wurin sunamai Allah ya sanya alheri gyada musu kai kawai yake dan baijin zai iya bude baki yayi magana ba ayanda yakejin kanshi sai Arham dake tayashi karban gaisuwan cikeda fara'a kaman shine ango, ganin kanshi yasoma juyawa yasa kaman an tsikareshi ya mike tsaye hannunshi cikin aljihun Arham hakan yasa da sauri Arham dake magana dawani yajuyo ya kallai, Waleed bai damu da kallon da Arham kemai ba yazaro key mota yay gaba da saurinshi yana tafiya kaman zai tashi sama yakarasa wajen motan su yabude ya shiga mazahnin6direna da sauri rabon dayay tuki da kanshi harya manta, harya tada motan Arham yazo ta wajen glass din yana kallonshi yace "are you crazy x-man? Where do you think u are driving yourself too? Bazaka tsaya ka gama amsan gaisuwan mutane ba zaka gudu kana ango? Banda hakama kaine zaka tuka kanka katuna the last time you drive?" tsayawa yayi kallon Arham for few seconds inyace zai bude baki yamai magana he might cry hakan yasa ya dauke kanshi ya sauke ajiyan zuciya sanan yawani irin fizgan motan yay reverse da sauri Arham ya matsa baya, ganin yanda aka juyo ana kallonsu yasa yadan saki murmushin yake yace "ahhhhm mantuwa ango yayi gift din dazai bama amaryan shi na daurin aure" murmushi duk akayi banda uncle dinshi dayane nan fari fat kaman bature yana sanye da manyan kaya da farin glass a idanu, yataho inda Arham din yake, cike da girmamawa Arham yace "sannu Uncle" cikin fada yace "ya akayi kabarshi yay driving kanshi so kake ka kashemana d'a?" wani irin dukan zuciyan shi maganan Uncle Arham yayi hakan yasa yadago Kanshi ya kalli uncle din ahankali, cikin fushi uncle yace "if u can't take care of our son wats the point of being his friend eh? Wlh bansan shirme mtdww" yaja tsaki sanan yajuya ya kwalama direban bodyguard din Waleed dake chan suna cin abincin su da gudu yataho yace "Allah taimaki yallabai gani" cikin fushi Uncle yajuyo ya kalli Arham din yace "ina yaje?" ahankali kaman wanda yake rashin lpy yace "I think gida yaje" "you think! What an insolence" Uncle yafada cikin bacin rai sanan takalli direba yace "drive home in Waleed nagida call me ka sanar dani, be fast he just left" da sauri direban ya shiga mota yaja shikuma uncle yajuya yakoma wajen friends dinshi akabar Arham shikadai awajen a tsaye idanunshi sunyi jazur, ganin yanda yan wajen ajikinsu ke kallonshi yasa ya kakalo murmushi yamusu yataho inda suke yacigaba da hirada su.

Cikin ikon ubangiji ya iso gida lpy, ta Gate din bayan layi yay parking tareda kashe motan, ahankali ya sauko yana ganin jiri yabude Gate din ya shigo ya shiga flat dinshi bedroom dinshi yawuce direct yawuce bathroom ya shiga kwara uban amai gwanin ban tausayi, saida aman ya

tsaya sanan yay flushing aman yabude tap ya kuskure bakinshi tareda wanke fuskan shi yajawo dan gajeren towel dinshi ya shiga goge fuska yana sauke ajiyan zuciya yafito, rage kayan jikinshi yayi jikinshi yadau mugun zafi ahankali yakarasa ya kwanta kan gado sai bacci.

Ahankali yaji ana kiran sunanshi sama sama ta cikin bacci, bude idanunshi yayi kadan ganin fuskar Arham yasa yabude idanun completely ya kallai, kafin ahankali yatashi ya zauna ya jingina bayanshi da bangon gado, zama Arham yayi agefenshi sanan ya fuzar da huci mai zafi kafin yadago kanshi ya kalle Waleed din yace "Waleed" Arham hardly call him da sunanshi saidai ya kirashi da Xman, yanda yakira sunanshi yasa ya kalleshi, anatse Arham yace "today is the last day dazan maka tambayan nan, wlh in bakaban amsaba bazan karabi ta kanka ba am telling you, bansan meke damunka ba, for god sake Waleed u weren't like this before, remember am your blood right, I know all ur worries, nasan anything that has to do with you, tun zancen auren nan naka ka chanza gabaki daya, I know magana dama namaka wahala but banda ni, amman this days harni din da kyar kake kulani, Waleed what is wrong? What's the matter with you? What is bothering you like this talk to me Waleed, talk! " Arham yadaka mai tsawa sosai, hannu yasa da sauri ya yatoshe kunnenshi saiga hawaye sun zubo, da sauri yasa hannu ya share, ganin hawaye akan idanun Waleed yasa jikin Arham yay sanyi ahankali ya matsa kusada shi yatsun shi biyu yakai kan fuskan shi ya dangwalo hawayen dayake kan fuskan shi ya kalli yatsunshi ganin hawaye ne da gaske yasa cikin wata irin muryan mamaki yace "t......tears X-man? Ar.....are you crying?" yay maganan da mugun mamaki dan zai iya cewa rabon dayaga kukan Waleed tun suna yara, cikin wata irin damuwa yace "Waleed wats making you cry like this? Baka rasa ci ba, sha ba, sutura ba, Waleed duk wata jin dadin zaman duniyan nan damuke ciki kanada shi, tari kadai zakayi sai sama da kasa ta kusan hadewa dan kawai asan dalilin dayasa kai tarin, look at your room" yabi ko ina da kallo adakin yace "dakinka ko dakunan 10star hotel albarka, everthing imported, designers kasa kaya mai tsada, kanada mesarati, ferrari, g wagon, brabus, benz, range rover wanan danake magana fa duk na 2020, kaci mai tsada, kahau mai tsada, ka taka mai tsada ka kwanta amai tsada, Waleed babu abinda kanema karasa aduniyan nan, kudi kaman zasu fasa account dinka, inda ace suna magana da naka harda fito zasu dingayi, banga abinda karasa awanan duniyan nan tamaliki yaumin deen ba u are loved banga wanda baya sonka ba, just look at how Ilham take sonka kaman zata mutu sometimes I use to wish inama nine kai dan banga wani abu dazai dinga damuna ba, koma abu nadamu na I can use my money na kauda duk wata matsala ta, money is problem solver and a  joy buyer" cikin crying tone Waleed yace "you are wrong Arham! You are wrong! You are so wronggggg" ya karashe maganan muryanshi tai rauni sosai, hannu yasa ya share hawayen dasuka zubomai tass sanan yakalli Arham da jajayen idanunshi yace "dukiya komin yawanta bata iya siya maka farin ciki, kwanciyan hankali, money can't buy happiness Arham, and right now right here, at this current moment I am not happy, I am not happy, I am very sad, very sad, kasan menene?" yay maganan yana goge hawaye dasuka zubomai kafin ahankali yace "I am not happy with this arrange marriage ko kadan na Ammi, shekaru na is just 28 maisa akeso amin aure? Am too young for marriage, gajiya akayi dani? Why rushing to get me into marriage, Arham am not ready for anything marriage nor am I  ready for anything family am too young, am not ready to settle down, inma aure ne baza abari na nemi wanda nikeso ba...." "to

kanada wacce kakeson ne Waleed kaida baka kula mata? U don't even have their time, rayuwanka gabaki daya you've dedicated it to your orphanage, ina kake gidan marayu, ina zaka gidan marayu, daga ina kake gidan marayu, beside what is dere da bazaka iya son zabin Ammi ba? That girl is beautiful, she is gorgeous, bata nemi komi ta rasaba na y'a mace ba, gata she's educated, tai karatu abinta, karatun ma a kasan waje, lawyer fa, haba in baka godema Allah ba ai baka bijirema ni'iman daya maka ba Waleed, ur wife is too perfect" cikin zafin zuciya Waleed yace "tunda har kaga perfection dinta marry her now? Wait! Are you on my side or side din su Ammi? My parents did awful things to me and u are supporting them? Where is my Arham my blood that always support me through thick and thin?" dan fuzar da iska Arham yayi saikuma yamika hannunshi yakama hannun Waleed din yace "am right here Waleed, am right here and I will always support you, always, I will always be by your side kaji" shiru Waleed yayi baicemai komiba sai kallonshi dayake idanunshi jajir, ahankali Arham yace "am not saying su Ammi sun kyauta, kuma am not taking side dinsu all am saying is the gurl is okay guy, kasandai u are still a virgin ko" yay maganan yanadan cizan lips dinshi alamun neman tsokana yace "kai har yanzu bakasan kan dadin abinva trust me this gurl u will enjoy her, kobaka sonta kadinga biyan bukatun ka da ita make ur self a man jor dan har yanzu kai boy ne" dan yatsine fuska Waleed yayi irin na shagwababbun yaran yan gayun nan yace "I can't sleep with a woman I don't have feelings for" cikin takaici Arham yace "kai matsalan ka kenan andai daura muku aure hakkinta na kanka dolen kane wanan wlh, anyway mubar maganan tashi kaje kai salla, ni zanje gidan naje naji mai kawayen Amarya ke bukata kafin gobe mu rakakai daki wayaga su Waleed ango, am even picturing how u will be groaning kaman giw......" jefamai filo Waleed yayi  Arham ya arce aguje yay wurin kofa yana dariya sanan .

[11/1, 11:46 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

_*DUNIYA BIYU MABANBANTA*_

✍️ M SHAKUR

7️⃣&8️⃣

_*This novel is 500 Fanmily*❤_

_How to Subscribe to TWO DIFFERENT WORLD_

_zaki turo 500 to account 3107021073 aisha Muhammad first bank, saiki turo evidence of payment to watsapp number na 07012181461, sainai adding naki a group din danake posting DUNIYA BIYU MABANBANTA, you can also send MTN card 500 idan bakida banki_

FREE PAGE

Fitowa tayi daga wanka daure da blue towel ganin Amah bata daki yasa tawuce tadau doguwan rigan da taciro ta shirya tsaf cikin rigan takarasa gaban dressing mirror taja kujeran ta zauna hannunta tasaka ta warware farin karamin towel din dake kanta gashinta ne yazubo daya saukan mata har waist gashin baki sidik dashi so silky irin gashinsu, wani brush tadauka dake gaban madubin tai brushing gashin dakeda sanstsi gashin nakara tsayi sosai brush kawai yawo yake acikin gashin, murmushi tayi ta kalli kanta dudda babu kwalliya akan fuskarta amman tai shegen kyau ribbon tadauka ta daure gashinta ta dunkule jelan gashin sanan ta mike tai wajen jakanta budewa tayi taciro mac book dinta da wayanta kiran iPhone wajen socket tayi ta makalasu ajikin chaji sanan tafito daga dakin kanta babu dan kwali, karasawa wajen mahaifinta tayi da duk suko juyo suna kallonta jin tafiyan ta murmushi tayi takaraso wajen ta zauna kusada Aby tana dafamai kafa tace "Assalamu Alaykum" "waallaikumu sallam" Aby ya amsata yana ijiye kofin shayin hannunshi akan farintin kofin, ashagwabe tace "Aby nikazubamin abinci na naci kasan ko I miss abincin gidanmu, abincin school baikai na gidanmu dadi ba, and a Egypt koda yaushe nikadai nakecin abinci kaman mayya, I miss eating abinci cikin yan uwana da babana da Amah, Amah ina Sabeeha?" Amah zatai magana sukaji sahun tafiya hakan yasa duk suka dago kai matar Aby ce tasauko daga stairs rike da dan karamin tray dake dauke da dabino da olives, murmushi ta sakan musu tace "Assalamu Alaykum, ahlan bikum" tai maganan tana ijiye tray agaban Aby, ahankali Aby yace "ahlan bik" murmushi Umm tayi ta zauna kusada Aby tanadan satan kallon Widad data sunnar da kanta kasa tana wasada flowers din kayanta kaman ba itace mai uban surutun nan yanzun nan kafin tazo wajen ba, maganan Aby ne taji akanta yace "yauwa Hibba zoki zubama yarki abinci yunwa takeji dan rigima kuma wai ni zan zubamata" yar dariya Umm tayi tajuya ta kalli Widad din tace "mezan zuba miki yar gatan baban ta?" faduwa gaban Widad yayi hakan yasa ahankali batare data dagokanta ba tace "Umm kibarshi dama wasa nake" ganin yanda tai magana yasa da sauri Aby yace "yaushe za'ai haka, bari nazubamana sai muci tare ko yarinyar babanta" baijira cewanta ba yazuba musu yadebo yashiga bata, shiru duk akayi kowa ya shiga cin abincin, dayake ka'ida ne basa magana in anacin abinci saida suka gamaci tsaf sanan ta tashi zata shiga tattare kayan Aby yace "leave it mamanki da yan aiki zasuyi, Ke magana zanyi dake zoki zauna, Hibba tashi ki gyara wajen nan" ba karamin ciwo maganan yama Umm ba amman saitai kaman bataji su ba yan aiki ta kwalama kira suka shiga kwashe kayayyakin abinci tana ga yamusu inda zasukai saida suka gyara wurin tsaf sanan yadan numfasa yakalli Widad dinda hankalinta yay nisa tanachan tana kallon wayanda ke raye raye a tsakar gidansu yace "Widad" juyowa tayi da sauri ta kallai da dara daran idanunnan nata, ahankali Abby yace "family Ahmad sun zo last week, although nina hana Ahmad karya fadamiki sabida nafison nafada miki dakaina, iyayen Ahmad sunason dansu wato Ahmad yay settling down, yariga yagama karatu dadaddewa so suke amuku aure inyaso shi Ahmad din can follow you chan Egypt din kicigaba da rayuwan ku kina karatu, nima nafison haka Widad so nake kiyi aure hankalina ya kwanta yanzu you are 20 this is just the right time, sai mukai deciding on yau ranan dakika dawo tunda dasafe zaki sauka da daddare sai ai engagement ceremony din in one week time kuma ai biki yakika gani yar albarka?" wani irin

kunya ne taji ya lullubeta batasan lokacin data boye fuskarta a bayan Aby ba tanadan murmushi, Amah tahau dariya tana tafi tace "wanan ayanda suke son juna itada Ahmad koyau kace zakai bikin su bazata taba cemaka a'a ba" akunyace ta tashi da gudu tai sama dakinsu ta fada tamaida kofar dakin ta rufe ta daura hannunta kan kirjinta dake bugawa da sauri da sauri, turo baki tayi saikuma ta harari system dinta tace "kojiya da daddare we did video call shine bai fadamin bako" tai kwafa saikuma tace "mun ma bata baran kiraka ba" ta daure fuska tabude kofa tawuce tafita chan rooftop din gidansu tahau babu kowa awajen sai gari dakeke gani ga iska na kadawa tako'ina, ahankali ta zauna tareda tan kwashe kafa ta lumshe ido tana feeling yanda breeze ke dibanta mamaki take dan she never thought of at this stage Aby zai mata aure, tazaci za'a bari tagama school kafin tai aure tunda duka duka saura mata shekara biyu, sosai tai nisa a tunani taji andafa mata kafada, da sauri ta dago kanta Aby ne, ahankali tace "Aby" zama yayi agefenta shima ya ta tankwashe kafa kaman yanda tayi yana kallon garin yanda mutane ke hayaniyan su cikin kwanciyan hankali yace "naje dakinku banganki ba nasan zan ganki anan saisa nabiyoki, Widad" Aby yakira sunanta anatse, dago kanta tayi ta kallai ahankali tace "na'am Aby" dan shiru yayi yana kallonta kafin yamika hannunshi ya shafa lallausan gashin kanta yace "inaso kifada min gaskiya karki ji kunya ta kinji, am your only friend right, inaso kifadamin kinason Ahmad?" shiru tayi tana kallon Aby kafin ahankali ta gyadamai kai, ahankali yace "mesa kike sonshi?" murmushi tadanyi ta dauke kai ta maida hankalinta kan kallon gari da sararin samaniya tace "Aby Ahmad is my best friend and only friend bayan kai, bayan Mama tarasu he was there for me giving me comfort, we use to play different games duddan kawai yaga bana tunani, anytime nafara kuka saiyaga nahakura nai shiru sanan hankalin shi zai kwanta, ko awayane saiya tabbatar daya lallasheni nahakura naidaina kukan sanan zai katse wayan, bayan nafada maka inaso naje karatu wani gari shima nafada mai he supported me, da ina Egypt kullum sai munyi video call, ya koyamin karatu, ya koyamin assignment, komi daya danganci na rayuwana he's there, he is just my everything my best best friend saisa nakeson shi Aby" tai dan murmushi saikuma ta daure fuska tace "but Aby yanzu fushi nikeda shi mun bata ma" da sauri Aby da tuntuni yake sauraronta yace "mesa?" murmushi tayi tace "Aby baifa fadamin his parents came over ba" dan dariya Aby yayi yakama kafadarta yasa hannunshi a aljihu yaciro wani dan karamin box yamika mata karba tayi tace "me aciki Aby?" cikeda jin dadi yace "open it" budewa tayi ahankali wani hadadden zobene na maza mai shegen kyau na gold tace "wow Aby, this is beautiful" tasa yatsanta tana taba ring din, anatse Aby yace "engagement ring dinki ne give it to your Ahmad kisamai a yatsan shi" dago kanta tayi ahankali ta kalli mahaifin nata kaman yanda yake kallonta hawaye ne suka zubo ahankali ta rungume shi bubbuga bayanta yayi yace "shiiii stop crying u are my everything Widad, am working hard in this life because of you if anything happen to you I will die, saisa nafison ayi aurenku ki koma Egypt tareda mijinki banson yanda kike zama a hostel ke kadai, I know Ahmad will always protect you he is a good loving boy" sun dade ahaka tana manne dashi jin ankira azahar yasa yasake ta tareda dagata yace "muje kiyi salla afara shirye shirye" gyadamai kai tayi yadagata suka tafi.

Suna saukowa falo daidai shigowan wata yarinya fara itama tarr doguwa tana sanye da bakin doguwan riga tadaura gyalen rigan akanta batare datai rolling ba ana ganin blonde gashinta hannunta rike da jakan makaranta, Widad na ganin ta washe baki tai wajenta da gudu tai kissing checks dinta starting from the left one taima right din sanan ta rungume ta tace "marhaba Sabeeha" hada ido Sabeeha tayi da Aby daya tsaya yana kallonsu murmushi tayi ta dago Widad din daga jikinta itama tai kissing din kumatun ta sanan ta shafa fuskarta cikin harshen larabci tace "iyye Widad kin kara kyau abinki, kin kara girma kaman bakeba, ya makaranta?" gyadamata kai Widad tayi tana murmushi tace "kema kinyi kyau Sabeeha" "Sabeeha" sukaji muryan Umm daga sama ta kwaloma Sabeeha kira hakan yasa ahankali Widad tasaketa duk suka dagokai harda Aby suka kalli Umm din dake gaban bene, dan murmushi tayi tace "abu zatamin ne sorry na katse musu hira, bari taci abinci saita sauka afara shirye shiryen da ita" gyadakai Aby yayi cikeda gamsuwa yace "hakane, wuce kije kiyi salla Widad bari naje masallacin nima" juyawa Widad tayi kaman yanda mahaifin nata ya umarceta tai dakin Amah itakuma Sabeeha ta gaida Aby ya amsata cikeda fara'a yanai mata barka da zuwa  sanan yawuce yafita dan zuwa gabatar da salla a masallaci.

Har daki Sabeeha tabi mahaifiyarta jakan makarantan ta tacire ta ijiye ranta adan bace tace "Umm maisa baki gayamin yarinyar nan zata dawo ba yau?" kofi Umm tadauka ta tittila mata madara a cup din sanan tajuyo ta mikama Sabeeha tace "nima uban nata bai gayamin ba nadaiga anata saka flowers ana gyara gidan nazaci ko yauma iyayen yaron nan zasu sake dawowa ne ashe itace shine dazu dasafe wai na shirya zamuje mu tarbo yar gaban goshinshi daga Airport" cikin fushi Sabeeha tace "shine ke kikawani je, ni wlh Umm bazan yarda Aby nawani treating naki kaman wata nani ba, ke nani yarshi ce kema ai matarshi ce mai matsayin da daraja, ni wlh bazan yarda ana wulakanta min keb....." da sauri Umm tace "ke jinan inhar zai mallaka miki dukiyarshi all his property yakoma naki ai zan iya komi, kinga daga Widad sai ke ku kadaine y'a y'a agidan nan, banda haka ke accounting ma kika karanta kuma yanzu ma final exams dinki kikeyi ke kikafi chanchanta da zama in charge of dukiyoyin shi ba yarshiba" dan murmushi Sabeeha tayi ta mikama maman tata Cup din milk din data shanye tace "Umm inabadai yau Widad zata fadi ta mutuba ta ina Aby zai mallakamin dukiyarrshi nida ba yarshi ba" murmushi kawai Umm tayi ta ijiye cup din tace "leave everything to me, tashi kije kiyi wanka kici abinci saiki sauka kasa wajenta, so nike kiyi amfani da ita hakan zaisa Babanta yakara miki wata daraja na musamman a fadanshi" dan yatsine fuska Sabeeha tayi tace "I can't stand that gurl Umm am so jealous of her wlh, I wish nikeda mahaifin mai sona irin Aby, I wish nikeda all abubuwan data mallaka" tai maganan tana bude dakinta tana shiga ta maida kofar ta rufe cike da rashin jin dadi, yayinda Umm tabi bayanta da kallo, wasu hawaye ne taji sun tarun mata a ido, tarasa maisa Aby baison yarinyarta kaman yanda yakeson Widad, kome Sabeeha take bukata yana mata, shike biya mata kudin makaranta ya ijiye mota na musamman da ita kadai ake kaiwa duk inda zata dashi, babu abinda Sabeeha ta nema tarasa kawai dai wanan son da kaunar da affection dayakema Widad baima yarta shi dudda Sabeeha ce kullum agidan but

baitaba jinta kaman Widad ba, baima janta jiki, daukan tray din madaran tayi tawuce ta shiga kitchen din dake falon ta dashi ta ijiye.

Shirye shirye akahau yi sosan gaske abunku da babban gida, ma'aikata ne daban daban kowa na aikinshi, shidai Aby na zaune a falo kan tattausan kujeranshi yana kallon Widad yanda take murmushi dimples dinta na lotsawa duka biyun tana kallon hannayenta da ake mata hadaddun lalle akai, kowani hannu da wanda ke mata lalle akai, itakuma Sabeeha ganin idanun Abba na kansu yasa ta shiga gyara mata dogon gashinta tana applying hair treatment din da aka gama hadamata na gashinta tana shafawa tana bama Widad labarin yanda take fitsari ajiki datana yarinyar Widad sai dariya take kaman cikinta zai kulle.

Sosai Abba ke murmushi yana kallonta deep down jiyake kaman karyama aurar da itan wlh baisan ya ai iya rayuwa ba itaba amman abu daya ke kwantarmao da hankali inya tuna shine yanda yaga tanason Ahmad din shima kuma Ahmad din na sonta, dafa kanshi dayaji anyi yasa yadago kanshi ganin Amah ce da sauri yatashi yazaunar da ita zama tayida kyau sanan ta kalli tsakar gidan dayake kallo tai murmushi tace "Widad kake kallo ko?" murmushi yayi yasake kallon inda Widad din take ya zubamata idanu yana murmushi yace "Amah she smiled just like her mother, Widad dina is so happy Amah" murmushi Amah tayi tana kallon Widad din da Saheeba ke saka mata gashinta cikin shower cap tace "nasan duk inda mahaifiyar ta take she's happy yarta is getting married" murmushi dukansu sukayi atare suka cigaba da kallonsu.
Gama zana mata lallen akayi sanan ta mike tsaye tana murmushi tahau rawa irin na yan mata dinan su Sabeeha namata tafi tana juyawa blouse dinta nasake zama umbrella, sosai Aby ke kallonta suna murmushi mawakan nasake rera mata waka duk wanda zai ganta sai yaji kaman ya saceta ya gudu she looks so adorable and so sweet and happy, ta gefen ido Sabeeha ta lura har yanzu Aby kallonsu yake hakan yasa ta tashi itama ta shiga filin sukahau rawa itada Widad din sosai Aby da Amah nata dariya.

Wuraren magrib aka gama raye raye aka wanke mata gashin ana wake akai drying gashin aka gyarashi tsaf bayan yasha maiyuka akamata parking sanan akasata taje tai wanka, wanka tayo sanan aka shiryata cikin wasu ubansu kaya long kaftan ne milk color dake dauke da stones da bids ta ko'ina masu shining kaman na diamond, djellaba (kaftan mai long lose robe) da aka daure mata igiyan ta wajen waist yay kaman belt, kayan kaman kayan yan India, aka yafamata gyalen kayan  aka bayan an gyaramata gashi anyi parking ansaka mata wata sarka ta gaban gashin anmata makeup mai kyau lips dinan anshafa mata red janbaki dayasa tai kyau kaman ita takera kanta, gusan sarewa da wakoki dasukaji yana tashi na welcoming groom's family yasa Sabeeha tace "Ahmad and his family are here, iyye ta Ahmad kinyi kyau" akunyace ta lullube fuskarta tana kara daure fuska ita adole Sabeeha tadena tskonar ta, Sabeeha tai dariya tace "ina platan dake dauke da zoben sa ranan?" ahankali tace "yana wajen Amah" gyadamata kai Sabeeha tayi tace "tom bari naje naga ya ake ciki awajen" fita tayi daga dakin tai dankareren

Kaman acikin mafarki yaji saukar wani tattausan lips kan nashi, bude bakinshi kadan yayi yay grabbing those soft tender lips yashiga kissing dinsu kaman zai cinye bakin, yatura tongue dinshi cikin bakinta yana lasowa kasa daurewa yayi yamika hannunshi trying to grab something yaji yakama mutum, ahankali yashiga bude idanunshi dasukamai nauyi kaman banashi ba, dishi dishi yake gani saikuma idanun suka washe tarr, ido da ido yayi da Widad da bakinta ke cikin nashi har lokacin bai dena kissing dinta ba idanunta sunyi jajir tsabagen kuka tana kallon idanunshi kuri kaman wata mayya, wani irin sakin lips dinta yayi da sauri yacire lafiyayyen hannunshi daga bayanta yaja jikinshi yakoma baya da sauri yana kokarin tashi zaune yana kallonta still, mikewa tayi itama tsaye takai hannunta kan idanunta tana share hawayen daya kasa dena zubowa sanan ta taho da sauri tazauna kan gadon tafada jikinshi ta rungume ta hanyar daura kanta kan kirjinshi tana kuka sosai, rasama mezai mata yayi hakan yasa yakai hannunshi mai lafiya yadaura akan bayanta yadan bubbuga alamun tai shiru sanan yatureta daga jikinshi ta tashi, hannunta ahankali takai ta daura kan wuyanshi dayaji ciwo tana turo baki kafin ahankali bama tasan tayaya maganan yafito daga bakinta ba tace "so....ry" gyadamata kai yayi cikeda dauriya, sanan ya tsareta da idanu, saikuma yace "who thought you how to do

that"? Yanuna mata bakinshi, juyawa tayi kaman wata yar yarinya ta nunamai TV da yatsan ta hakan yasa ya kalli TV, Korean film yaga anayi yasan tunda ta nunamai wajen yasan anan tagani, shiru yayi yana kallonta, muryan Ammin shi dayaji yasa ya kalli kofa da sauri, faduwa gabanshi yayi, hakan yasa ya kalleta, dagata yayi tamike tsaye, anatse sabida tagane cikin harshen turenci yace "inaso kidauki Teddy ki ki koma dakinki kinji Saheeba, anjima kadan zanzo wajenki, now be a good girl and listen to me and go" makemai kafada tayi tafashe da kuka, girgiza mata kai yayi kaman zaiyi kuka yace "please Saheeba kitafi, yanzun nan zanzo kinji" sake makemai kafada tayi tana kuka, ahankali yasanya hannunshi ya jawota jikinshi rungumeta yayi tareda bubbuga bayanta a kunnenta yamata whispering yace "listen to me, please Pretty go, I don't want Ammi to see you here, please pretty go" yay maganan tareda dagota ahankali, fuskarshi ta kalla ya gyadamata kai hakan yasa ta sauka ahankali daga kan gadon, daukar Teddy dinta tayi sanan tajuyo ta kallai shima kallonta yake kaman yau yafara ganinta, ahankali tasa hannu tabude kofar dakin tafita tamaido kofar tarufe yana kallonta, ta glass din kofar yacigaba da kallonta ahankali take tafiya ta kankame Teddy ta, tai corridor dazai sadata da ward din da aka kwantar da ita. Ajiyan zuciya ya sauke tareda lumshe ido yadaura hannunshi kan fuskarshi kafin yasauke hannun kan bakinshi yay shiru yana tunanin what just happened.

*******

Within 30min IGP yayi deploying police zuwa address da Ammi ta tura mai. Knocking Gate din gidansu Arham one of the police men yayi, fitowa daga daki maigadi yayi yaleko, ganin police ne yasa yace "bayin Allah wakuke nema"? Wani daga cikinsu ne yace "Goodday please we are looking for Mr Arham" mai gadi da tuni jikinshi yahau bari ganin yan sanda yasa yace " yes gidan nan ne gidan Mr Arham" daya daga cikinsu policeman dinne yace "is he in"? Ware ido mai gadin yayi dan baigane turencin ba hakan yasa daya daga cikinsu yace "yana nan? Da sauri yace "yes.....eh,yana nan, yanzun nanma ya shigo gidan" "kaimu wurin shi" da sauri yajuya yay gaba suna biyedashi abaya har flat dinsu yabude kofa yashiga suma haka, a palour suka sameshi ya daura kafa daya kan daya yayi resting head dinshi a kam one seater kujeran dayake zaune akai hannunshi rikeda chilled maltina, jin mutane akanshi yasa yadago yana kallonshi, babban su ne yace "good-day  Mr Arham we are here to invite you to our office for some questioning" yana gama maganan yafito mishi da ID card dinshi ya nunamai, bin ID card din yayi da kallo sanan yatabe baki yamaida kanshi kan kujeran yana girgiza kafa, kara maimaita mishi maganar sukayi but no response still saima maltina shi daya cigaba dasha, mai gadi ne saya gama tsurewa yace "Alhaji dakai fa suke" dago kanshi yayi ya musu wani irin

kallon banza yace "what questioning"? Cije lips policeman din yayi yace "when you reach our office you will find out" "and where is your office located at"?

Shiru police din yanasa baicemai komiba dakin ya tsit, maigadi dake shirin sakin fitsari yace "Alhaji kabisu kar su maka wani mara kyau, kagan sunata binka ahankali tun dazun, kawa Allah kamike kabisu" y
policeman dinne ya juya ya kalli wasu manyan officers guda biyu da sauri sukai heading directing to kujerar da Arham yake zaune. "Sir you are under arrest" fisgoshi daya daga cikinsu yayi ya tayar dashi tsaye Arham bayyi wata wata ba ya dauke policeman din da mari mai kyau, bai ijiye hannun kasa ba yaji saukan mari to ko'ina akan fuskarshi dayaji yaji kwakwalar warshi tajuya abaibai.

❤❤❤
[11/1, 11:48 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍ M SHAKUR

3️⃣0️⃣

Kamar jira suke suka haushi da duka kaman an aikosu suna bugamishi gindin bindiga all over his body, jin duka tako'ina yasa Sadiya tafito daga ciki dagudu tana ganin Arham ya sanda ke duka tahau ihu, mai gadi shima jikinshi narawa yashiga rokonsu su yakuri subarshi amman ko jinshi basayi saida suka tabbatar da sunmai lilis, he is totally weak baima iya motsi jini nafita daga hancin shi da bakinshi sanan suka barshi suka sakamai ankwa handcuff sanan suka jashi kamar ragon layya suka fita dashi daga dakin zuwa cikin motarsu.

Binsu har waje Mai gadi yayi shida Sadiya suna rokonsu akan susakeshi amma basubi takanshi

ba, suna jefashi ciikin motarsu suka shiga direba yatada motar sukai gaba dashi.

Koda suka Isa police station fuskar Arham yay subu subu tsabagen mari kan dayasha, janshi suka karayi zuwa cikin station din suka bada report that lead them har suka mishi dukkan nan sanan aka jefashi cikin cell, babban su ya shigo cikin cell din rikeda wata zungurariyan takarda ya fara karanto mai offense dinshi na trying to murder Dr Waleed warbai.   Janshi akayi zuwa toture room aka Fara tambayarshi why he strangulated Mr Waleed Warbai. Dago jajayen idonshi Amma baice musu komai ba.  Fara dukkanshi sukayi tako Ina Yana ihu Yana " Don Allah kuyi hakuri, it was a mistake"  kuka yafara yi Amma still basu barshi ba. Sai dasuka tabbatar da sun mushi lis har kasa daga lafanshi guda dayayi sannan Suka kawo mishi ruwan zafi suka bashi yasha.

Bayan sallan magrib Ammi da Mom da Mama suka shigo dakin dan sunje masallaci sunyi salla, ganin Waleed azaune yasa da sauri Ammi ta saki jakanta kasa tazo gadon tazauna gefen kafafunshi takai hannayenta kan fuskar Waleed, kaman zata fashe da kuka tace "My baby katashi, tell me meke maka ciwo eh? A ina kakejin ciwo ajikinka, tell me Waleed dina meka maka ciwo"? Tai maganan hawaye nata ruwa a idanunta tana shashafashi kaman zata cinyeshi, dan murmushi yamata ganin yanda tadamu yace "am fine Ammi karki damu, meya kawoku orphanage haka? Mama" yakira sunan Maman Arham ahankali yana murmushi, karasowa Mama tayi wajen zuciyarta tamata mugun nauyi, wani irin kunyan Waleed dinma taji tanaji jibi yanda danta yamai, yaron dake sonshi dake nufinshi da alkhairi ne yama wanan jina jinan, tsayawa tayi ahankali agabanshi, dan murmushi tayi mai kama da murmushin dole sanan ahankali tahada hannayenta biyu tace "Waleed dan girman Allah kayakuri abinda Arham yamaka, wlh naji kunyan halin......" da sauri Waleed yamika hannunshi mai lafiya yakama hannun Mama yace "Mama me haka kike cewa dan Allah? Please kidena bani hakuri, ninace miki Blood yamin wani abune"?  Wani wawan harara Ammi ta watsa mishi, Mama tace "Arham yamaka abinda ba daidai ba, Arham bai kyauta ba, kalli halin dayasaka ciki, wlh naji kunyan abinda yamaka, kunyan kallonku dukama nike, Arham bai kyauta ba wlh, saisa nabama Ammi goyon baya takiramai yan sada amai lilis akaryashi kaman yanda shima yamak......" kafinma takarasa maganan Waleed yatareta yace "waya kirama Arham police"? Cikin fushi Ammi tana ballamai harara tace "nice nasa aje akamashi akaishi police amishi shima dukan dayamaka, ko angayamai banison kane dazai kama yamaka wanan dukan eh? Karfinku dayane yasan da shekara nawa ya girmeka dazai kamaka ya bubbuga haka saisa nasa inspector yasa aka kamashi akaishi Station amai wanan shegen dukan dayamaka" sosai idanun Waleed sukai wani irin ja ranshi yawani irin baci, cikin fushi yace "Ammi wai mesa in everything saikin shiga rayuwana ne eh? Friends fight don't they? Sabida munsami miss understanding da blood saiki shiga fadanmu har kisa akulleshi, ninace miki ki kullemin dan uwane eh"? Wani irin kallonshi Ammi take kaman ta rufeshi da duka amman bazata iyaba, wani irin kunci da haushin abinda

Ammi tasa akama Arham yaji hakan yasa yace "Ammi call that inspector right away kicemai yasaki Arham" cikin fushi Ammi itama tace "bazanyi ba dan ubanka" Waleed zaiyi magana da sauri Mama datake ganin duk laifin ta ne komi tace "kaga Waleed abinda mahaifiyar ka tayi tayi gaskiya, daidai tayi wlh ko ansakoshi nida kaina saina sassaba mishi, dan haka kamabar maganan nan" gyada musu kai Waleed yayi cikin kunan rai yace "ok" wani irin yunkurawa yayi daga gadon yana cije baki sabida yanda bayanshi da kafadarshi da aka daure ke mugun ciwo, da sauri Ammi ta tareshi tace "kai ina zaka Waleed" ture hannunta yayi cikin karfin hali irin na maza ya shiga kokarin sauka daga kan gadon, rikeshi daga Mama har Ammi da Mom sukayi, fashewa da kuka Ammi tayi tace "Waleed wai mesa bakajin magana ne kacika taurin kai eh? Ina zaka, sokake daurin da aka maka ya turgude, Waleed kasheni kakeso kayi kahuta eh Waleed, mena maka? Mena maka nace da zaka tashi zakabar gadon da kake kwance kana ganin bamaka da karfin tashi" tureta yayi a haukace ya kabar da hannunta daga jikinshi yace "leave me alone Ammi, kurabu dani, I can't fight with my friend again, friends can't fight again? Eh dole saikun shiga, dole sai kin shiga komi nawa? Ko kasheni Arham yayi he's my friend, Ammi you have no right to interfere in my affairs, sabida Arham ya dakan saiki aikamai police su kamashi a kulle shi adaka haba Ammi, haba Mom" yay maganan yana kallon Mom itama yace "bakuji kunyan Mama datake nan tsaye dakuba kuna saka a chaza danta eh?" da sauri Mama zatai magana Waleed yadaga mata lafiyayyen hannunshi yace "Mama please kiyi shiru" sanan ya kalli Ammi yace "Ammi baki kyautamin ba, and inhar you feel wanan abun dakikeyi akaina shine son dakike min then guess what am not proud of the love you have for me am not, cus kinsa inajin kunyan abokina, my childhood friend, my only friend my blood Ammi, Ammi you hurt me today" yay maganan yana kwanciya a gadon ahankali tareda lumshe ido, shiru Ammi tayi tana kallonshi kalaman shi sun mugun sosamata rai, zatai magana Mom ta girgiza mata kai, dauke kai tayi tace "Waleed nikake ma magana haka akan nace a hukunta Arham ko" tai shiru tana kallonshi ko bude idanunshi Waleed baiyiba, ciro wayarta tayi takira Inspector agaban su tace asaki Arham din sanan ta katse wayan, sanan ta kalli Mom tace "stay with him nizan tafi gida" tana maganan tadau jakanta cikeda fushi tafita daga dakin zuciyarta kaman zai tsage yafashe, Mom zata bita Mama tace "bari nina bita ki zauna dashi" juyawa Mama tayi tafita daga dakin, Mom kuma ta zauna kan kujera takifa kanta kan gado tai shiru tana tunani.

Koda Mama tafito har motar Ammi direba yajata sunyi gaba, awani irin hankali Mama takarasa motarsu, baya tabude ta shiga direba ma baya cikin motar da alamu masallaci yaje, fashewa da kuka tayi sosai, intace dukan da Arham yama Waleed bai mata ciwo ga wlh tai karya, ta bala'in jin ciwon dukan nan kaman me, Waleed d'a ne wlh, dan halas d'a na kwarai, tasan harga Allah tanaso aramamai amman da Waleed yafarka yayma Ammin shi maganganun nan saida ranta ya sosu, bala'in sosuwa ma, Waleed d'ane da kowace uwa zatai alfahari dashi aduniyan nan, taji kunyan abinda danta yamai wlh taji kunya, tasan Ammi tagaya mata maganganu amman ko kadan bataji zafinsu ba dan tasan ciwon dakake ji in wani yakama maka d'a yadaka ba gaira ba dalili, Arham bakin halinshi da bakin zuciyanshi tamai yawa, kuka tayi mai suna kuka amotar nan hakanan ma taji bazata iya komawa cikin asibitin tahada ido da Waleed ba, tana zaune direban ta ya shigo yace "Hajiya yakuri ina masallaci ne mutafi?" gyadamai kai tayi tace "eh

mutafi", tada motar direban yayi suka fita daga gidan marayun.

Direban Ammi nakaiwa gidan bamata jira yabude mataba tabude tafito, ahankali take tafiya dan bamata gani sosai, kanta wani irin bugawa yake kaman ana dukanshi da gatari, falo tabude ta shiga, yar aikinta da gudu tafito tana mata sannu da zuwa ko iya amsata bata iya tayiba tawuce stairs tai sama ahankali tabude dakinta ta shiga, yarda jakanta tayi anan tsakiyar dakin tawuce kan gadonta da kyar ta zauna tamika hannunta ta shiga tattaba saman kan side drawer dinta wani goran magani ta dauka da sauri, sanan ta bude taciro wasu kwayoyin magani na masu hawan jini guda biyu ta jefa abaki ta hadiye sanan tadauko bottle water ta kurbi ruwa kadan tasha, kanta na bala'in ciwo, tadafe kan da duka hannayenta ba'awani dauki lokaci ba bacci yay awon gabada ita.

***

Wuraren karfe biyun dare cikinta yawani irin murda mata da sauri tabude idanunta rass ta tashi zaune tznabin dakin da kallo, fuskarta ta taba taji tahada wani uban zufa kaman wacce tai dambe dudda uban AC dake dakin, tashi tayi ahankali ta dauki wayarta ta lalubo number Waleed tana yatsine fuska sabida ciwon maran datakeji, dailing number shi tayi amman bai shigaba, hartai bacci taga bai dawo ba gashi number ta bayi shiga hakan yasa tamike tsaye ahankali da kyar tana daga kafarta tabude kofa tafito daga dakinta, dakin Waleed tabude taga baya ciki hakan yasa tai stairs tafara tafiya ahankali zata sauko, wani irin ciwo dataji ya tokare mata mara yasa ta kurma wani mahaukacin ihu. "Mai gadiiiiii" zama tayi awurin tana wani irin nishi kafin tasake kwalama mai gadi kira, akaro na uku ne yaji yafito daga dakinshi yana share idanunshi dake cikeda bacci, ganin daga flat ake kiranshi yasa yay flat din yabude kofa ya shige hango Ilham daga ita sai doguwan rigan bacci yasa yay wurinta da sauri yace "Hajiya sannu haihuwan ce bari nakira miki dakta awaya" zai ciro wayarshi tace "kabarshi bayi shiga, kiramin duk wanda zaka iya kira azo a kaini asibiti azaba nikeji mai gadi" takurma wani uban ihu da saida ya firgita yace "Hajiya salati zakiyi, salati ake" juyawa yayi ganin bamatasan inda kanta yakeba ihunta kawai take, saida ciwon yadan sarara sanan ta nemi number Arham amman harya gama ringing bai dagaba, sau biyar takirashi amman shiru, dialing number Ammi tayi shima bayi shiga, ganin haka yasa tai dailing number Mummy ta, ringing daya Mummy ta tadauka fashewa da kuka tayi tace "Mummy mutuwa zanyi, Waleed bai dawo gidaba number shi bayi shiga, ina kiran number Maman shi itama bata shiga, dagani sai mai gadi agidan, kuma bai iya tuki ba balle yakaini asibiti, Mummy mutuwa zanyi" tafashe da kuka sosa daya ruda mahaifiyarta, anatse tace "kinga ba'a kuka in ana nakusa, be strong kinji yar albarka, ga Babanku nan yanzu zai kawoni wurinki just stay where u are kinji am coming" ta katse wayan, daidai mai gadi na shigowa yace "Hajiya wlh duk basa bude gate kinsan anguwan manya ne nan" ko jinshi batayi tahau ihu tana kuka sosai mai gadi yama rasa maizai mata sai dialing number Waleed yake amman bata shiga.

Wani ruwane yafashe mata dayasa tahau ihu. "mai gadi zan mutu kataimaka min wayyo Allah na kataimaka min dan Allah, daidai lokacin akai knocking kofar gidansu, da gudu mai gadi yafita yana zuwa yabude gate iyayen Ilham dinne mamanta da Babanta} da mota, Mmummy ce ta shigo tai ciki tafito da ita aka sata a motar Baba sanan takoma ciki taje ta nemo akwatin haihuwan ta adaki sanan tawuce takai motar ta shiga baban su yaja motar sai hospital.

Bakaramin wahala tasha ba sai wuraren karfe 8nasafe ta haihu, ta haifo danta namiji katoto mai bala'in kamada Arham kaman yay kaki ya tofar.
[11/1, 11:48 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍️ M SHAKUR

3️⃣1️⃣

Shirya yaron akayi aka fito da fitoda shi aka kawoma Mummy shi, ahankali Mummy ta karbe shi tana murmushi tace "miji nasamu ko kishiya"? Dariya nurse din tayi tace "miji ne Hajiya" karbanshi Mummy tayi tana kallonshi yaron kato dashi Masha Allah.

Daidai mijinta yakaraso tace "Alhaji kaga mijina masha Allah dawa yay kama"? Dan dariya Alhaji yayi yace "ai kamanshi daban da uwar da baban, hala sai nan gaba zai dauki kamanni, sake gwada namban mijinta dana mahaifiyar shi kiji ko zasu samu yakamata" number Waleed tafara dialing amman bai shiga har lokacin hakan yasa tai dialing number Ammi, lucky wayar ta shiga, wayar na gab da katsewa Ammi ta dauka, kafin ma Ammi tai magana Mummy tace "kawata lpy kuwa? Tun jiya da daddare muke kiranki dagake har Waleed baya shiga wlh hankalina yatashi" dan murmushi Ammi tayi tace "Waleed ne yadan sami hatsari wlh yana asibiti agidan marayun shi har karyewa yayi akafada, ban fadima Ilham bane kinsan mai ciki ba'a daga musu hankali haka, nikuma ina dawowa gida magani nasha na kwanta sabida hawan jinina yatashi, Mom ce awurin shi amman yanzu nai wanka shiryawa ma nike nakaimusu

breakfast" da sauri Mummy tace "innalillahi wa innailaihi raji'un, ashe abinda yafaru kenan Ilham takira takira mijinta bayi shiga daga karshe saidai takira mu mukazo gamunan a asibiti wlh tasami karuwa yanzun nan amman tun cikin dare mukazo, anmiki miji fa, baki ganshi ba dan lukuti dashi" Mummy tafada cikeda farin ciki sabida tasan yanda Aminiyarta keson jika, Ammi mutuwan zaune tayi tama kasa magana, hakan yasa Mummy ta kyalkyace da dariya ta kalli mijinta tace "Alhaji tayi mutuwar zaune fa" sukahau dariya sanan tace "ki shirya saiki biyo kiga jikanki kafin ki kaima su Waleed abinci, Allah yabashi Ipy, anjima dazaran an sallameta zamuje mu gaidashi"

Ammi kasa yarda da abinda aka gayamata tayi hannunta har wani irin rawa yake tai dialing number Mom dake zaune dakin tana kallon Waleed da tun jiya daya lumshe ido yaki budesu bacci mai nauyi ya kwasheshi yanzu muka yatashi dan tasan yana jinta sarai wlh, kaman bazata dauki wayan Ammi ba saikuma ta dauka takai wayar kunnenta, wani irin zabura tayi tace "Ilham ta haihu?" rass Waleed yabude idanunshi jin ance Ilham ta haihu, katse wayan Mom tayi tana murmushi sanan ta kalli Waleed dake kallonta ta tabe baki tace "mara kunya aika bude ido dakaji matarka ta haihu, suna asibiti ta haihu ansami namiji" ahankali yadan saki wata yar kyakkyawan murmushi sanan ya yunkura zai tashi, kafadarshi kawai da akai dauri kehanashi motsi yanda yakeso, da taimakon Mom ya iya tashi, Mom tace "me kakeso?" ahankali yace "office dina zani, I want to shower na chanza kaya naje nagansu" taimaka mai Mom tayi yamike tsaye ahankali suka fito waje, nurses sai gaidashi suke gyadamusu kai kawai yake, haryakai kofa yatuna alkawarin dayama Widad, Mom ya kalla yace "am coming Mom" sanan yay hanyar dakin datake, hannunshi yasa yabude kofar ahankali yashiga yana kallonta ganin tana bacci, ahankali yakarasa gaban gadon ya tsaya akanta yana kallon fuskarta kaman yatasheta dan taganshi saikuma yafasa yajuya kawai yafito tareda kullo mata dakin sanan yafito yay office dinshi shida Mom suka shiga ciki, dakin shi ya shiga yay bayi, brush yayi sanan yay wanka da ruwan zafi, jikinshi ciwo yakemai bana wasaba bai taba fada a rayuwanshi ba ko saisa Arham yay galaba akanshi oho, fitowa yayi yadauko wani jean yasaka da kyar sanan yadauko wata riga sai saka yakasa sawa, kwalama Mom kira yayi hakan yasa ta shigo, wani scissors yanuna mata, saida suka yanke hannun rigan daman sabida hannunshi yay balance sanan tasamai rigan ta shinfidamai dadduma yay sallolin da ake binshi sanan suka fito, Mom kejan motar suka dauki hanyar asibitin da Ilham take, parking sukayi suka fito sanan suka fara tafiya har zuwa dakin datake akwance.

Bude kofan Mom tayi ta shiga, Ilham na kwance kan gado, fuskarta ya kumbura suntum tsabagen kuka, sai Mummy dake zaune kan kujera rikeda jaririn da aka shirya yay kyau, Mummy na ganinshi tace "subhallahi, innalillahi wa innailaihi raji'un, Waleed wanan wani irin hatsari ne kaga yanda jini yataru a idanunka kuwa, jibi wuyanka da fuskarka sannu Waleed" kanshi akasa duk take maganganun nan ahankali yace "ina kwana Mummy" "ina kwana Waleed, ya karfin jiki? Allah yabaka lpy kaji, Allah yasa kaffara ne sannu" gyada matakai yayi suka shiga gaisawa da Mom sunama juna barka, karasawa gaban gadon yayi yana kallon Ilham data tsareshi da ido itama tana kallonshi tana mamakin abinda yasame shi haka, dan murmushi yamata ya shafa goshinta da hannunshi saida ta lumshe ido tabude su ahankali ta kalleshi,

murya chan kasa yace "thanks for giving me a baby khadija, Allah yamiki albarka" gyadamai kai tayi tareda mika hannunta takama lafiyayyen hannunshi tarike gam, cikin muryanta da baya fita sosai tace "what happen to you Babyna"? Baki yabude zaiyi magana Mom ta taho rikeda jaririn tace "wato agaban mu ake nuna mana sonkai ko kana nuna kafi damuwa da matarka kan yaronka dayazo duniya yauko" murmushi Mummy tayi ranta fess ganin Waleed naji da yarta. Mom tamikamai yaron tace "ga danka nan dauki abinka kaga yanda yay kama da abokin ka kuwa kaman yay kaki ya tofar" wani irin mummunan faduwa gaban Ilham yayi saikuma ta daure ta lumshe idanunta da sauri kaman wacce bacci ya sace, ahankali Waleed yasa hannunshi ya karbi yaron yana kallon fuskarshi sanan yazauna abakin gadon yana rikeda shi yana kallon fuskar jaririn dake bacci yana murmushi, ko Allah yasan cewan yanason Arham, so na domin Allah, Allah ya azurtashi da d'a amman sai yaron bai biyoshi ba bai biyo mahaifiyar shi ba saiya dauko kamannin amininshi hakan yasa yaji bazaima iya sakama yaron sunan mahaifinshi ba, dan da yace in namiji yahaifa zai sakamai sunan mahaifinshi but wanan da yaron ke kama da Arham dole Arham zai bama yaron kodan Arham yagane shibai rikeshi da komiba sanan har gobe har jibi shi dan uwanshi ne no matter what.

Bakinshi ya daura kan goshin yaron ya sumbaci yaron yana murmushi sanan yama yaron huduba ya karbi dabinon dasuka sayo da zasuzo yatauna yabama yaron yabashi ruwan zamzam, yadago kanshi ya kalli Mom yace "Mom sunan d'ana Arham Waleed Warbai" shiru Mom tayi tana kallon Waleed din for few seconds itama Ilham saida tabude ido gabanta nafaduwa ko Waleed yagane ne saisa yabama yaron sunan Arham sosai ta birkice saikuma cikeda siyasa tace "d'ana yawani kama yayi kama da abokin ka saikuma kawani bashi sunan shi" karban yaron Mom tayi tace "Allah ya rayaka Arham, daidai nan aka bude kofa Ammi ce ta shigo yar aikinta abayanta da direba rikeda basket din abinci, tace "ku yakuri ai danaji ya'ta ta haihu kitchen na koma da kaina namata abincin da maijego yakamata taci, sassanunku now ina Dr da nurses din dasuka karbi haihuwan jikana kuga" tawuce tafita waje tana kwalama nurses da Dr kira, duk wanda yazo bashi bandir din yan dari biyar guda take zukuga yanda aka cika Mummy sai murmushi take, saida ta rabar da kudin tass sanan ta shigo dakin ta kalli Mummy Ilham tace "bakin ciki kikemin ne aminiyata bazaki tashi akan kujera na zauna na dauki jikana ba"? Kwashewa da dariya akayi, Mummy ta tashi daga kujeran tace "maida wukan dadin abin nidai kafin nayi wanan jikan naki nayi wasu balle amin yanga" zama Ammi tayi tace "yanga yanzu kika fara gani" all this maganganun ko Waleed dake zaune bata kalla ba, saisa ma bataje gadon ta duba Ilham ba sabida yana wurin, ahankali Mom ta taho rikeda Arham junior sanan tamikama Ammi shi ahankali tace "ga Arham Waleed Warbai, Arham karami" Mom tai maganan tana kallon fuskarta kaman yanda itama Ammi tadago tana kallon fuskar Mom kafin ahankali tadaura fuskarta kan yaron, shiru tayi ganin yaron kaman Arham yay kaki, dudda yaron jariri ne but kamannin was so obvious da kana gani zaka gane da Arham yake kama, gabaki daya Ammi jitayi duk wanan farin cikin da murnan nan da rawan jikin datake yi na zatazo taga jikanta yakoma ciki, abinda ma yafi bata abin shine sunan dataji Waleed yasamai, kuma tai alkawari bazata sake shiga rayuwan shiba kaman yanda yafadi, so yasaka sunan abokinshi ma danshi danyaci mata mutunci itakuma bazata cemai komiba ya kyauta, murmushi kawai tayi tace "Allah rayaka Ar.....an jikalle" tafadi ahankali danta kasa kiran sunan Arham din, bude kofa akayi Baban Ilham ya shigo ciki yana ganin Waleed yace "assha, sannu son wanan daurin asibiti ai

saikafi shekara baka warkewa tashi muje nakaika wajen wani mai dauri yana maka zaka warke cikin sati tashi muje" yay maganan yana kallon Waleed tashi yayi ahankali yabita gaban Ammi da kanta kekan jaririn, suka wuce suka fita, a mota baban Ilham ya daukeshi sai janshi yake da hira amman baya wani iya amsawa da kyau dan nauyin mutumin yakeji, agaban wani gida yaga sunyi parkin, fitowa sukayi baban Ilham yace "muje" shiga sukayi har wani dankareren falo inda wani mutumi ke zaune, Baban Ilham yace "Barka da rana malam, ga dana nan ya karye akafada munzo agyaramai" tashi baban yayi yazo yadaura hannunshi kan wajen saida Waleed ya yatsine fuska sabida zafi, Baban yace "ba karaya bace kashi ce ta goce ina gyarawa yanzu shikenan" da sauri Baban Ilham yace "kagani ko babu abinda asibiti suka iya indai kan dauri ne, yace Baba ayi mun gode" kwalama wasu maza kira Baba yayi, Waleed yaga wasu karfafan maza su kusan shidda sun shigo, hannu Baba yasa ya warware daurin sanan aka rike Waleed din, addu'a Baba yayi yatofa kan kafadar sanan yakai hannunshi kan wajen yafar kokarin saita kashin sosai Waleed yaso yadaure dayaga azaban ba nan bane yafara kokarin kwace kanshi amman ko motsi baya iyayi, da azaba yay azaba kuka yafara kaman zai mutu Baban Ilham sai sannu yakemai kusan awa daya aka dauka a hannun sanan baban ya gyara tsaf aka sakeshi da sauri yasa hannu yana share hawayen Baban Ilham sai sannu yakemai, magani Baba ya shafamai akafadar yace "ka warke baka bukatan wani dauri kuma angama" kudi Baban Ilham yaciro mai yawa yabiya mai sanan suka tafi.

Duk suna zaune adakin Dr ta shigo ta duba Ilham sanan tabasu sallama tawuce tafita, ahankali Mummy tace "aminiya natafi da ita gida tai jego ne?" ada Ammi tai alkawari bazata je jegon gidaba amman sai kawai taji gwara sun tafi, gyama Mummy kai tayi tace "eh kuwuce kuma a kulamin da matan d'a da jika da kyau, suna arba'in zanzo na kwashi abuna wlh" duk akai dariya Mummy tace "nina nafi kowa sanin bala'in ki ai bazanyi wasa ba yallabiya" tai maganan tana kallon kofa ganin anbude Baba ne da Waleed da idanunshi sukai jajir da sauri Mom tai wajen Waleed din tace "sannu Dan Yaro an gyara" gyadamata kai yayi, Baba yace "bama karaya bace ashe gocewar kashi ne yanzu an gyara an shafamai magani, Allah yabashi lpy" ahankali Mom tace "angode Alhaji" Mummy tace "Allah baka lpy" itadai Ammi tai kaman bataji su ba, Mummy ne tace "Alhaji an sallamemu mutafi dasu gida, agida zatai jego" da sauri Baba yace "to bari nakai kayan mota" daukan kaya yashiga yi Waleed yaje zai tayashi da sauri Baba yace "kaga jeka zauna kaida hannu ba lafiya ne zakadau abu jeka huta" yay maganan yana fita, ganin haka yasa Mom ta shiga tayashi suka kwashe komi sukakai mota, sanan Waleed yadau hijab yabama Ilham tasaka ahankali yace "test me all that you need zan aiko miki dashi" murmushi tayi ya gyadamai kai ganin yana wani ji da ita kodan ta haifamai d'a ne, kofa yabude mata tafita suka jera atare tana tafiya ahankali har motar Baba ta shiga ta zauna sanan ya matsa ganin Ammi tazo baby ta shiga ta bama Mummy sanan suka rufe musu motar suka tafi Ammi tajuya tai motar ta ta shige direba yajata banda Waleed daya tsaya chak awajen, ahankali Mom tace

"mutafi" daga kafa yayi yawuce ya shiga motar ta suka tafi, gida sukaje yana fitowa flat dinshi yaje kwanciya kawai yayi, yaciro wayarshi number Arham yakira amman harta gama ringing bai dauka ba, 3 miss calls yamai ganin bai dauka ba yasa yamai message.

_"Hey blood, I called no answer I guess you are still angry with me, I called nafada maka Khadija ta haihu, an sami baby boy, yaron yay kama dakai sosai blood, and do you know what's even} great? Yaci sunanka, sunanshi Arham Waleed Warbai, blood you mean alot to me, u make my life colourful, I am sorry idan maganan dana maka jiya kajita somehow I was just trying to know what you've been up to lately, and I am also sorry akan abinda Ammi na tamaka please forgive us, take care, anjima  zan shigo_"

Yaturamai sakon tareda lumshe ido bacci na saceshi kafin baccin yay nasaran daukeshi.
[11/1, 11:48 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

💫💫_*DUNIYA BIYU MABANBANTA*_💫 💫

✍️ M SHAKUR

3️⃣2️⃣&3️⃣3️⃣

END OF FREE PAGE
Wuraren karfe biyun rana ya farka, sosai yaji karfin jikinshi kawai gajiya yakeji bawani abuba, tashi yayi dagakan gadon yaje gaban madubi ya tsaya ya kalli kwayar idanunshi na dama ganin har yanzu akwai jini aciki yasa yabar gaban madubin yana tunanin inya fita anjima zai tsaya a pharmacy yasai maganin dazai saka jinin idanun ya washe, bathroom ya shiga, wanka yayi yasake yin brush sanan yafito, wardrobe dinshi yaje yadauko wasu native, farin yadi ne mai taushi da akamai jumper yasaka sanan yadau turare yafeshe kanshi dashi, dadduma yahau yay sallan azahar sanan ya zira takalmi bayan yadauki wallet dinshi yafito, side din Ammi yayi

gabanshi nafaduwa, ahankali yabude kofar ya shiga hada ido yayi da Ammi dake zaune kan dogon kujera hannunta rikeda remote ko taji zai shigo ajikinta ne oho dayasa take kallon kofar oho, suna hada ido ta ijiye remote din ta tashi daga kan kujeran da sauri ya shigo dakin yamaida kofan yarufe yace "Ammi, Ammi please wait" sama Ammi tayi da sauri yabita kafin yakai harta shige dakinta tarufe da key dan bamata son ya shigo, tsayawa jikin kofar yayi yay shiru, yakai kusan 5min ahaka sanan yace "Ammi please listen to me, kiyakuri kinji please Ammi na" yay maganan ahankali yana knocking kofarta yakai kusan 10min ahaka awurn ganin bamata da niyyan bude kofan yasa yawuce ya sauka kasa, dinning yaje yazauna sabida shegen yunwa yakeji, warmer yabubbude, tuwon shinkafa yagani da vegetable soup, zubawa yayi baima wani iyaci da yawaba yasha ruwa yamike tsaye key motar Ammi dake kan centre table yadauka yawuce yafita, motar ta ya shiga ya zauna sanan yaciro wayarshi ganin har lokacin Arham baimai reply din message dinshi ba yasa yatada motar direba yabude mai yawuce yafita daga gidan.

Agaban gidansu Arham yay parking motarshi yabude yafito yatura gate ya shiga gidan, babu kowa a tsakar gidan, sallama yayi yabude kofa ya shiga falon Mama ce ta amsa mai ahankali, saikuma tasaki murmushi tace "Waleed kaida bakaji sauki bane ba kafito? Ya karfin jikin? Maman ka takirani ta sanar dani abin farin cikin daya samemu ubangiji Allah ya raya, ya dayyaba, ya sunan yaron ne"? Murmushi yayi yace "sunanshi Arham Mama" wani iri Mama taji jikinta yay sanyi, sanyin ma karara hakan yasa tama kasa magana, lurada yanayin ta yasa Waleed yace "Mama ina Arham yana nan"? Cikin dan fushi tace "ohon mai rabona dasa Arham a idanuna kwana uku kenan yau" mikewa da sauri Waleed yayi yay corridor falon shiga yayi direct yay gaban dakin Arham, knocking kofar yayi yakirashi. "blood" jin shiru yasa yatura kofar ahankali ya shiga cikin dakin, dakin babu haske sai uban duhu, ahankali yamika hannunshi ya kunna switch hakan yasa dakin yya haske, Arham ya hango kwance kan gado bai lulluba ba dagashi sai gajeren wando fuskarshi ta kumbura suntum tsabagen dukan dayaci, jikinshi duk tabon ciwo dawani irin sauri Waleed yay gadon yace "subhallahi blood who did this to you eh? Waya maka haka"? Yay maganan yana dago Arham zaune, tashi zaune Arham yayi yana wani irin kallon Waleed din da sauri Waleed ya sauka yay bayinshi, ruwan zafi ya dauko yajefa towel ciki yazo yazauna akan gadon cikeda tausayi ya matso towel din kaman zaiyi kuka yakai kan fuskarshi yana dannamai yace "blood am so sorry, am ashamed of abinda Ammi na tasa aka maka, look what they did to you, this people are heartless, sorry blood" yay maganan yana gaggasamai, ijiye ruwan akasa Waleed yayi bayan yagama yasauka daga kan gadon yanabin dakin dayay kacha kacha da kallo yace "kasha any medication, kaci abinci?" dudduba dakin yayi ganin baiga maganin anything ba yasa yadau ruwan yakai bayi yafito sanan yadawo kan gadon, hannunshi yadaura kan kafadar Arham yana kallonshi kaman yanda Arham din ke kallonshi, ahankali yace "talk to me blood meke maka ciwo eh? Sanan wani abinci zakaci let me go out and get it for you, kafada min please ina da ina ke maka ciwo mow"? Wani irin kallo Arham kemai kafin ahankali yakai hannunshi ya kabar da hannun Waleed daga kan kafadarshi yace "wato halinka Waleed naban mamaki" ahankali Waleed na kallonshi yace "halina blood kaman ya"? Dan murmushi Arham yayi yakai hannunshi ya share fuskarshi dahar lokacin lema leman ruwan da Waleed u gasamai jiki kekai yace "kaida uwarka kunsan polisawa sunzo sun

kamani sunmin bugun mahangurba shine yanzu zakaso kana wani rawan jiki kana bani kulawa kaman bakasan hakan yafaru ba" sassauta murya Waleed yayi ahankali yace "blood listen to me, I have no reasons to lie to you koda chan banmaka karyaba yanzu ne zan maka karya, believe me bansan Ammi tasa amaka abu makamancin hakaba, a lokacin danasani saida nasa aka janye aka sakeka, blood you are my only friend danai basing life dina dashi in this world, bazan taba hurting nakaba no matter what, besides you are morethan a friend to me, you are my blood Arham" tabe baki Arham yayi sanan ya nunashi da yatsa yace "ku masu kudin nan feels zaku iya duk yanda kukaga dama aduk lokacin dakuka so, zaku iya duk yanda kuka so aduk lokacin dakukaga dama, listen to me Waleed wlh zan gwadama aduniyan nan dudda uban kudinga, kadaiga mahaifinka nada kampany akasan waje dake gina boat dawasu kampanoni, mahaifiyarka nada kampany da business da dama ko, amman wlh zan nuna maka duk wayan nan kudin da dukiyan dakuka tara bazai taimakeka da komiba saika gane kurinka Waleed" shiru Waleed yayi yana kallon idanun Arham, all he could see was hatred, tsantsan tsana kawai yake gani a kwayar idanun Arham, wani iri yaji yanaji kaman zaiyi kuka saikuma yahana kanshi, ahankali yana kallon Arham din yace "Arham all wanan fadan da maganganun is it akan kawai natambayeka ina kake kai kudin ka? But why do I feel kaman there's more to this case, blood na kalli idanunka abu daya kawai nake gani shine tsantsan tsana ta, blood mena maka? Menataba maka? What have I done to you please kafadi mini watakila bansani ba please tell me kaji my friend" da sauri Arham yanuna kanshi yace "friend? Nine friend dinka Waleed? I can never be a friend to rich kids sabida all they know is sumaka ihu, suyi controlling naka, suyi matching naka and step your your neck aduk lokacin dasukaga dama, Waleed zaka iya tuna how many times kakemin ihu kakemin tsawa in your office kanamin fada"? Wani irin hawaye ne Waleed yaji sun gangaromai shaaarr, hannu Arham yanunamai yace "ba kuka nace kamin ba tambayanka nayi, kasan how many times kakemin ihu aka a office"? Girgiza mai kai Waleed yayi ahankali kafin yafuzar da iska yasa hannu ya share idanunshi tass sanan yanisa yace "I never meant all those shout, badan cin mutunci kowani abubane yasa nayi hakaba, Blood kasanni sama da kowa, and you know how passionate I am towards my work at the orphanage, idan yazo takan orphanage dina ne banson wasa kawai strictly work saisa I do all those to you sabida kai aikin da yakamata kayi, but tunda har ahaka kadauki abun ka fassara am sorry for that too I didn't do it because am rich or whatever I do it cus I feel is my own way of motivating my staff to do more, to perform better, idan akazo kan human resources management akwai two ways of motivating a staff, akwai positive motivation and negative motivation, I guess mine was the negative one but kayakuri" ya karashe maganan ahankali muryanshi tayi sanyi sosai, tabe baki Arham yayi yace "orphanage orphanage orphanage, staff, staff, staff, Mr, Dr. Waleed Warbai the chief CEO of Warbai orphanage home and home of the disables how does the name sound"? Yatambayi Waleed dake kallonshi cikin yanayi na isgilanci sanan yaydan murmushi yace "I will make you a promise yau dinan akuma gabanka, Waleed kome kaci sai Arham yaci! Waleed kome kasaka sai Arham yasaka! Waleed kome kahau sai Arham yahau! Waleed kowani matsayi ka taka sai Arham yataka shima! Sai last thing dazan fada maka is over between us" da sauri Waleed ya kallai, gyadamai kai Arham yayi yace "yes is over tsakanina dakai Dr Waleed Warbai, we should go our separate ways, yanzun haka danake maka magana my resignation letter na gidan marayun ka duk lokacin dakaje za'a baka, ka kama gabanka nakama gabana, daidai da silebiyar dinka karka sake bama Mahaifiyata, Arham bai sanka ba bai san dazaman

kaba kaima do me a favour ka kwatanta hakan, is over we are not friends we are not friends, please katashi kafitar min daga daki kabar min gida and yau yakasance rana ta karshe dazaka kara zuwa gidanmu" kasa koda motsi Waleed yayi daga inda yake, hannu Arham yadaga yanuna mai kofar dakinshi yace "out, I said out" yadaka mai tsawa irin na cin mutuncin nan yace "indai kai ba maye bane katashi kafitar min daga daki mara zuciya kawai dolo" sosai Waleed ke kallonshi kafin ahankali yasauka daga kan gadon idanunshi sunyi ja mugun ja yabude kofa ahankali Mama yagani gaban kofan, murmushin dole ya kakalo yace "sai anjima Mama" baima jira amsanta ba yawuce yafita da sauri yya wajen gate yafita yabar gidan ya shiga motarshi yaja dawani irin gudu sanan yabar anguwan.

Bin bayan Waleed Mama tayi da kallo taji gabaki dayan maganan su sabida ita kanta tadamu tun ranan batada Arham a idoba sabida fushin datake yi dashi yasa taki zuwa tadubashi, hakan yasa Waleed na shiga dakin tabiyo bayanshi.

Tura kofan dakin tayi ta shiga, hada ido tayi da Arham da yana ganinta ya saukar da kanshi kasa, ahankali dawata irin murya dake rawa sosai Mama tace "Arham Waleed kama wanan cin mutuncin, Arham anya nina haifeka kuwa? Anya nonon nan nawa kasha"? Takama nonon ta tanunamai, saikuma tafashe da kuka sosai dan her heart is so heavy tace "wlh wlh da'ace a asibiti na haifeka Arham da na rantse maka da Allah dayau dinnan sainace bakaine danda nahaifa ba, anchanza mini kai a asibiti, amman agida na haifeka dagani sai unguwar zoma" tafashe da kuka sosai, sanan ta share idanunta tass da bakin zaninta tace "wlh albasa batai halin ruwa ba, babu ta inda ka gado malam mahaifinka, baban ka malami ne, wayan nan manya manyan malaman da ayau a Abuja dasu akeji duk ubanka ya koyarda su Arham, Arham ubanka malami ne, kakanka malami ne, amman kaiko Arham shaidanin yaro ne" tafadi haka tsabagen yanda zuciyarta ke tafarfasa, cikin ihu da fada da kunan rai tace "Arham wai shinko katuna waye Waleed koko kamanta ne?" tamai tambayan tana kallonshi sanan tace "Arham kanajin tsoron Allah kuwa? Arham kana kokarin ka tabbatar da cewan mutane kadau mutum daga rana ka maidashi inuwa shi saiya maida kai rana, Arham kai butulu ne eh? Yanzu inda ace zaka tashi kaje sip dinan naka zan rantse da Allah nakuma kara idan akwai kayanka daka saya da kudinka basu wuce kala biyu, Arham gabaki dayan sitiranka Waleed kisiya maka, Arham yaron nan nasonka har kuka naji yana maka kanamai ihu kana cewa ba kuka kace yamaka ba, matarshi ta haihu yarada ma danshi sunanka Arham duk baka ganin abubuwan nan? Da ace Waleed bai tsamoka daga talauci dahar yau ayaba kake saidawa, Arham Arham Arham" Mama tama rasa maizata cemai saikuma tafashe da kuka tace "kaga yanda idanun yaron nan suka taru da jini dukan dakamai? Amman bai rikeka ba ya tattako yazo wajenka, bari kaji bazan taba bari ka

wulakanta mai sonka ba wlh, bazan taba bari ka wulakanta wanda ya chanza mana nidakai rayuwa ba, Arham bazan taba bari ka wulakanta Waleed ba domin ka wulakanta yaron nan kadauka nika wulakanta aduniyan nan, dan haka dau wayar ka ka kirashi agabana kasa handsfree dan naji, kabashi hakuri sanan kafadimai duk abubuwan daka fadamishi wasa kake kanajina "! Mama ta dakamai tsawa, dago idanunshi Arham yayi ya kalli Mama yace "Mama kiyakuri amman wlh ni bazan kirashi ba, kuma kidena cewa ya taimake mu babu abinda Waleed yamana Allah ne yataimake mu kuma shine yamana komi wlh, daman shi Allah haka yake abinshi inya tashi taimaka maka saiya nemo wani ya taimaka maka ya hanyar shi, tunda ai shi Allah bazai sakko kasa yamika maka kudi da hannunshi ba yace gashi Arham saidai yay amfani dawani, dan haka wlh Mama ni Allah ne yamin komi babu wani mahaluki daya isa yataimaken, Shidin banzan shi, kudin shi na banza meyake dashi, shi idan ma yaga asalin masu kudi guduwa zaiyi yaboye wlh irinsu Otedola, Zuckerberg da sauransu, shidin me shidin banzan shi, dan ubanshi nada kampani a kasan waje yake mana kapapa yana daga mana kafada wlh bazan kirashi ba" yay maganan ranshi duk abace, rungume hannu Mama tai aciki tana kallon Arham kaman tasami TV, ahankali Mama tace "Arham Annabi yace a kullum mudinga kallon nakasa damu bana sama damu ba hakan zaisa mungode ma Allah da kyau, Arham batun yau nake karantan wani abu tattare dakaiba amman yau Allah ya bayyanamjn abin gabaki dayanta Hassada kakema Waleed" da sauri Arham yana daga murya yace "shi awa zan tsaya inamai hassada Mama? Ubanme yakeda shi? Allah ya kyauta kafin na ganshi naga masu kudi dubu ni mama kima dena min maganan wani Waleed banson jinta, dashi da wanan matsiyaciyar uwarnan nas...." bai karasa maganan ba Mama taxuba ma bakinshi mari, sanan tacire slippas din kafarta tahau dukanshi ta ko'ina tace "Arham kaci uwaka, bani na haifeka ba, wanan bakin halin naka da bakar zuciya uwarka da ubanka basu dashi, wayanda suka taimake ka kake zagi eh, kai wani irin butulu ne, Arham ni kake so kabama kunya aduniyan nan" dudda dukanshi take bakinshi kin mutuwa yayi yace "ki kasheni Mama, dama batun yau nasan kinfison Waleed kan danda kika haifa ba, Waleed nada kudi, yasai miki gida da mota, gaki da generator ga solar, ga kayan abinci ga kudin kashe wa ba dole ba, Mama ki kasheni sabida Waleed, badai danni banda kudiba banda gidan marayu ba saisa bakisona nima ba zakiga abinda zai faru Mama kicigaba da dukana har saina daina numfashi, badai kowa dukana yake akan Waleed dan gata ba, ajebota kucigaba nikuma namuku alkawarin sainaima Waleed abinda dukanku bazaku iya taimakon shiba wlh, wlh kuwan, kiyita dukan" yakara mika mata kanshi dantaji dadin duka, dukanshi Mama tayi har saida Sadiya taji ta shigo da gudu taja Mama baya dake haki kaman zata mutu tace "sadiya kibarni na kashe yaron nan nahuta dan ba da'na bane, Sadiya kibarni, Arham nason yacimin mutunci, Sadiya Arham nason ya kunyatani aduniya, dawani idanu yakeson na kalli mutanen nan dasuka mana komi a rayuwa eh" tafashe da kuka, rungumeta sadiya tayi itama tahau kuka tace "Mama yakuri kidena kuka dan Allah" cikin wani irin fushi Arham ya tashi ya finciki key motarshi yafita daga dakin ya barsu awajen idanunshi sunyi jajir.

Waleed rasa inda zashima yaji dadi aranshi yayi kirjinshi sai wani irin mugun tafarfasa yake, baisan ya akayi ba yadaiga yazo gidan marayun shi, parking motarshi yayi yafito sai gaisheshi ake yama kasa amsasu da sauri da sauri yake tafiya har zuwa cikin asibitin shi, direct ward din da Widad ke kwance yake, bude kofar ahankali Ya shiga maida kofar yayi yarufe yana kallonta ganin bacci take, direct yawuce gadon da sauri zama yayi kan plastic chair gaban gadon kawai yakifa kanshi kan gadon kukan dake cinshi tun adakin Arham ya shiga sakinshi awajen ahankali yana sheshek, maganganun Arham gets to him sosai, sun shigeshi was he that bad kaman yanda Arham ya suffanta shi? Was he?.

Kaman amafarki taji kaman ana kuka ahankali wanda sautinshi ke kaiwa har kokon kirjinta, bude idanunta tayi kaman wacce ta firgita ta kalli ko'ina kafin ta kalli gefenta, kan mutum tagani kife kan gadon, gashin kan nawani irin shining sunyi sili sili tsabagen gyara dasuka ji, dudda bataga fuskarshi ba amman tagane mutumin nanne bargon jikinta tayaye da sauri taja jikinta ahankali ta tashi tazauna tana kallonshi tai raurau da ido, ahankali tadaga hannunta ahankali tadaura akanshi, jin soft hannu dake dauke da dan danshi danshin zufa akan sumanshi yasa yadago kanshi ya kalleta da jajayen idanunshi da hawaye yacikasu sosai, wani irin kallonshi take hankalinta yatashi sosai ganin yana kuka ahankali yakai hannunta kan fuskarshi sharemai hawayen tayi da sauri tana girgizamai kai, jiyayi zuciyarsshi tawani irin tsinke baisan lokacin daya tashi daga kan kujeran yazauna abakin gadon ya rungume cikinta tsam ba, fuskarshi nakan cikinta yasaki kuka ahankali cikin harshen turenci yace "Saheeba baki sanni ba, dudda duka yanzu 10month kikayi da sanina, dan zaman dakikayi tareda ni please ki gayamin am I a bad person? I know I makes different decisions, but kowani decision zan dauka abune dazai kawo cigaba dakuma raya wanan gidan marayun, you know ana yawan cewa breakup masoya ne kawai irin couples haka ke breakup ba'asan cewa akwai friendship breakup ba and the shit hurts badly" yasaki kuka sosai akan cikinta dayasa tahau girgiza mai kai tana bubbuga kanshi alamun yay shiru tana kokarin magana takasa but kana ganinta kasan ta mugun damu, ahankali yace "I am so saddd, I don't know who to talk to, banma san mesa nazo wajenki ba bayan bazama kingane menake cewaba, but crying ajikinshi anyway makes me feel better, am sorry natashe ki kinji" yay maganan yana dagowa daga jikinta tareda tashi daga kan gadon yana juyawa da sauri batare dayabari sun hada idoba, hannunshi yaji anrike gam hakan yasa ya tsaya chak, dirkowa tayi dagakan gadon tana rikeda hannunshi ta zagayo tagaban shi ahankali ta tsaya tana kallonshi, gani yayi itama idanunta sunyi ja, ahankali tabude bakinta tana kallonshi takai almost 20sec tana kokarin iya maganan dazatayi sanan cikin yar siriruwan muryanta tace "you aren't a bad person" tai maganan tana kara kai hannunta yakama dayan hannunshi tarike gam, sanan ta kallai tace "you are a goodman" tai murmushi dayasa hawayen idanunta suka zubo, saikuma ta washemai baki tace "and I love you" tasakin mai wani heart melting murmushi dayasa all her dimples suka lotsa, wani irin ajiyan zuciya yasauke yasan bamatasan metake cewaba, sanan this is not the first time ake cemai I love you besides Ilham tasha fadimai kalman nan countless time but yau da Saheeba tafadi saida heart dinshi yakusan skipping out, like he felt the words har cikin diddigan kashin jikinshi sosai yay nisa yana tunani yaji an fizge hannunshi, firgigit ya farka yaga ita ke janshi, zaunar dashi tayi akan gado ga mamakin shi

daiyaga tasa hannayenta akan kafadarshi ta turashi ya kwanta tana murmushi, samun kanshi yayi da kwanciya yana wani iri kallon yanda takemai murmushi kaman yau yafara ganinta, stethoscope din dayake dauka kullum dake kan bed drawer dinta inya shigo dubata ta dauka ta makala a kunnenta tsaf tana murmushi sanan tazo bakin gadon tana ware Big lulu eyes dinta ta daura hannu kan lips dinta tana kallonshi alamun yamata shiru sanan takai bakin stethoscope din ta daura kan saman kirjinshi ta saman riga lumshe ido yayi da sauri yana sauke wata nauyayyan ijiyan zuciya jin hannunta kan jikinshi, ita kawai she is doing it jokingly ne but jin beat din kirjinshi acikin kunnuwan ta yasa tawani irin kwalalo ido a tsorace ta fizgo daga kunnenta ya yar, dan dariya yayi yatashi yazauna ahankali itama dariya tayi saikuma ta makemai kafada ta taho dagudu tawani fada jikinshi ta daure hannayenta tabayanshi tana murmushi, wani irin natsuwa ne yaji ya shige shi, lumshe ido yayi tareda manna hancin shi cikin gashinta, murya chan kasan makoshi yace "I love you Saheeba".

_*This novel is 500 Fanmily*❤_
_How to Subscribe to TWO DIFFERENT WORLD_
_zaki turo 500 to account 3107021073 aisha Muhammad first bank, saiki turo evidence of payment to watsapp number na 07012181461, sainai adding naki a group din danake posting DUNIYA BIYU MABANBANTA_

_Zaku cigaba da ganin update , cikin satin dazamu shiga in shaa Allah, ONE LOVE FANMILY_
[11/1, 11:48 PM] Re@l🖤 K@usy 🔐: 💫 _TWO DIFFERENT WORLD_ 💫

✍️ M SHAKUR

3️⃣4️⃣

*This novel na kudi ne, idan kika karanta baki biya ba banyafe ba🤷🏻‍♀️*

_*This novel is 500 Fanmily*❤_
_How to Subscribe to TWO DIFFERENT WORLD_
_zaki turo 500 to account 3107021073 aisha Muhammad first bank, saiki turo evidence of payment to watsapp number na 07012181461, sainai adding naki a group din danake posting DUNIYA BIYU MABANBANTA_

Dagokanta tayi da sauri ta kalli fuskarshi tana kwalalomai idanunta irin meyace dinan dan batasan meyace ba, taji yay magana but bataji meyace ba dan ahankali yay maganan, har lokacin hannayenta kulle abayanshi tana kara kallonshi, manyan kwayoyin idanunta farare tass ya kalla dayaji sunsa jikinshi ya soma mutuwa, ahankali yakai yatsanshi yadan dungure matakai yace "bazan maimaita abinda nace dinba kina kallona da manyan idanunki da basu dade da dawowa daidai ba" washe mai baki tayi kaman tasan maiyace dan hausa yamata, tsayawa yayi yana kallon set din white hakoranta yace "lemme go" yay maganan yana kwance hannunta dake bayanshi yadawo dasu gaba, yamike tsaye da sauri, kaman zatai kuka ta rikemai hannu karbe hannunshi yayi da sauri ahankali kaman mai shirin bata tsoro yace "stop touching me anyhow Saheeba ba kyau"

